[5/21, 7:52 PM] Matar 'Dan Aljannah: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*123*
Asp ya hangi abinda yake shirin faruwa! cikin 'karaji! yace." Umaru kada ka harbi kan domin hakan ba hujjah bane."

'Dakin yayi tsit! tsananin tashin hankali ya hana su aikata komai!

Asp yaja jiki da rarrafe ya iske gurin da yake tsaye har yanzu bindigar na wuyansa.

Ya rike kafafunsa jikinsa na wani irin karkawa yace." Na fada maka kada ka harbi kanka Umaru zaka mutu kafuri domin abunda ka aikata a yanzu ba haram bane jahadi kayi kuma kayi dai-dai domin karshensa kenan a kashe shi kamar yanda ka kasheshi saboda haka ka cire bindigar nan daga wuyanka."

Dr Salihu dake tsaye jiki a sanyaye yace." Wannan magana haka take ranka ya dade kada ka aikata aikin daka sani kayi hakuri mu jin dadin abinda kayi a yanzu kuma muna alfahari da hakan."

Gabad'aya hayaniyarsu ta cika dakin kowa yana fadin albarkacin bakinsa.

Zazzafar ajiyar zuciya ya sauke ya juya yana kallon gawar a kwance tayi muni! fuskar ta kara 'baki babu alamun rahama a tare da gawar!

Dr Salihu ya iso gurin a hankali ya cire bindigar daga hannunsa, ajiyar zuciya ya sauke da sauri ya matsa daga gurin, fita yayi yaje adana bindigar ya dawo dakin.

Lokocin likitocin sun rufu kan Asp suna bashi taimakon gaggawa!

Umar din ya tsugune gaban Gawar! yana dubata.

Dr Salihu ya tsuguna da kayan aiki a tare dashi.

Binkicen gawar yayi sosai nan ya tabbatar da cewa ya mutu mintina ashirin da suka wuce.

Ya kalleshi da fadin." Abin mamaki da al'ajabi ko ya akayi wannan takadirin ya samu nasarar shigowa asibitin nan."?

Murmushin takaici yayi kafin yace." Idan nace Najeria babu tsaro sai a musanta!  handama! babakere! cin hanci! zamba! cikin aminci cin amanar 'kasa! zalinci! duk ya tattara a wannan 'kasa shuwagabbani kuma suna kallo. Dr Salihu ko shakka ba nayi wannan d'an ta'addan dake gabanmu yana da d,caurin gindin shuwagabbani."

Dr ya sauke zazzafar ajiyar zuciya da fadin." Yau dai  karya ta kare wai bori ya kar boka gashinan a kwance ka alkadarinsa   wannan babbar nasara ce a gareka amma a ina zamu samu cikakken bayani.

Shuru yayi na minti biyu kafin yace." Akwai sanya hannun Dr Shu'aib ina zarginsa."

Dr Salihu ya jima yana kallonsa kafin a sanyaye yace."  Amma ban ta'ba tunanin cewa Dr Sha'aib zai ci amanar aikinsa ba tsayin shekaru goma yana aiki ba'a ta'ba kamashi da wani laifi mai muni ba sai a wannan lokacin yana da kyau dai ayi binkice sosai.

Yaja dogon tsaki da fadin." Idan babu sanya hannunsa babu yanda za'ayi wannan dan iskan ya san in da nake, bari na sheda maka cewa kai tsaye da nufin kisa ya shigo dakin sai kuma yayi rashin sa'a! ni na kasheshi babban burina kenan naga gawarsa a kwance a gabana."
Cikin karsashi da kwarin gwiwa yayi maganar!

Dr Salihu dai gabadaya jikinsa yayi la'asar tausayin Abokinsa ya cika masa zuciya,  wannan shi ake kira da mugun ji! ko mugun gani! ba shakka azal! ce ta ritsa da abokinsa amma kaf tarihin rayuwarsa bashi da wani tabo Dr Shu'aib mutumin kirki ne kowa ya sheda hakan.

Washe garin ranar da al'amarin ya faru  gari ya d'auka  Asibitin ya cika da mutune da kuma 'yan jarida babban burinsu a bar su su shiga domin su dauki  hoton gawar sannan kuma su samu zantawa da Jarumin da ya kawo karshen d'an fashin daya Addabi kasa.

Labari har fadar shugaban k'asa  cewa a daran jiya *GOJE!  ya samu nasarar kashe UBAN DABA!* wanda ya addabi 'kasa da ta'addanci sai dai kafin ya  samu nasara a kansa sai da sukayi dauki ba dad'i!  anan ya  samu nasarar galabaitar da kakakin rundunar 'yan sanda Jahar

katsina wato Asp Musa Baharu yanzu haka dai yana kwance ana bashi taimakon gaggawa."

Mai girma shugaban kasa yayi farin cikin faruwan hakan, ba kuma tare da bata lokaci ba ya tura wakilansa domin zuwa su tabbatar da al'amarin kana kuma suyi jinjina tare da mik'a gaisuwa da godiya da yawunsa.

Comissinoner ya kasa zaune ya kasa tsaye! jikinsa sai rawa yake bakinsa ya bushe tsabar fargaba da tashin hankali sun ha nashi sakat! sa'i da lokaci gabansa sai ya yanke ya fad'i! watakila ya tattara kayansa ya gudu shine kawai kwanciyar hankalinsa.

Umaru shi da kansa ya bada Umarnin d'aure Dr Sha'aib a cewarsa a gurinsa za'a samu duk wasu bayanan da ake bukata.

Da farko dai gardama ya fara, sai suka cire imani da tausayi suka fara laftarsa! babban mutum da girma da iyali sukayi masa tik! suna masa tujara! duka ko ta inaa!.......Yana kuka da hawaye da majina ya daga hannuwasa da fadin" Ku saurara zanyi bayani."
Suka saurara da dukan da suke masa. wasu zafafan hawaye masu zafi suka fara tsare a saman fuskarsa.

A daddaure! aka shiga dashi dakin.

Sun kai su ashirin a tsaye a kansa!

Asp dake kwance a hankali ya tashi yana kallonsa sosai yake mamakinsa! fuskar salihai gareshi ba za kayi tsammanin zai aikata wani mugun aiki ba.

Umaru kuwa yana tsaye ya goya hannuwansa a baya. shima mamakin Dr Shu'aib din yake, wai dashi aka hada baki domin ganin bayansa.

'Yan jarida biyu maza da mace daya suka shigo dakin da kayan aiki a tare dasu.

Ganin shigowarsu yasa kai tsaye ya nufi gurin da Dr Shu'aib din yake gurfane! gumi yayi masa dabaibaiyi.
*(Allah mugun ji da mugun gani Allah ka karemu)*

Ya tsuguna gabansa a nutse ya kira sunanshi.

Cikin tararrabi da damuwa ya kalleshi bakinsa ya bushe tsabar wahala!

Zuciyar musulci gabadaya sai tausayinsa ya rufeshi, amma bai nuna a zahiri ba, ya sha kunu da fadin." Dr kayi mana cikakken bayani gamu gabad:aya ga kuma manema labarai shin ya akayi *Uban daba!* ya samu damar shigowa asibitin nan da mummunan kudiri, ya shigo dakin da nake kwance jikinsa sanye da kayan aikinka yanayin hallita ya sanya da yawa mutane basu sheda waye ba saboda basaja! shin ya akayi hakan ya faru."?

Ya jima kansa ya sunkuye yana dawurwura! kafin da kyar yace." Umaru kaddara ce ba halina bane wallahi azal ce ta afka min."

Yace." Duk na yarda da maganarka amma kasan cewa idan da kaddara tabbas akwai son zuciya a ciki akwai sanya hannun shugabbani a tunani sunyi maka alkawarin makudan kudi shin ko ba haka bane."?

Maganar a kan hanya take, wannan ne dalilin da ya sanya ya kasa furta kalma guda. tabbas hakane.

Yace." Shurun ka na nufin maganata a kan hanya take."

Ya kalleshi idonshi jawur! ya tara 'kwallah! yace." Umaru babu ruwan shuwagabbani a cikin wannan al'amarin. abunda na sani shine mai girma Commissioner naku shi yayi tattaki ya sameni har cikin gidana da mummunan kudirinsa.

Cin amana ba halina bane. ba a shedar kai amma tunda nake ban ta'ba yunkurin cin amanar aikina ba sai a wannan lokacin. nayi mamaki mutuka lokaci guda na amince da manufarsa. a take yayi min alkawarin miliyan goma bayanshi wani babban dan kasuwa Alhaji Mutari mai zinare yayi min alkawarin miliyan ashirin mutukar na amince da manufarsu.

Nan na tambayesu dalilin da yasa suke bukatar ganin bayanka.

Dukkaninsu suka tabbatar min da manufarsu....Commissioner yana adawa da yanda Allah yayi maka d'aukaka! yayi maka baiwa! ya daga darajarka! duniya ta sanka manyan mutane suke alfahari da kai! a cewarsa yana ji a jikinsa watarana zaka iya gadar kujerarsa ko kuma ka iya mulkar kasar baki daya. to wannan dalilin yasa yake jin haushinka yake bukatar ganin bayanka a doron duniya.

Alhaji Muktari mai zinare  ya tabbatar min da cewa.  kai ne kayi sanadiyar tattalin arzikinsa, wannan dalilin yasa ya sanya ido akanka har ya samu nasarar samun labarin asibitin da kake kwance.
A take suka had'u shi da Commissioner suka sauya min ra'ayi!  suka rinjaye ni na amincewa bukatarsu.
Wannan shine abunda ya faru." Cikin rauni da rashin confidence ya 'karasa maganar.

Asp ya kalleshi da fadin." Dr Shu'aib kaci amanar aikinka! bayan haka kuma kaci amanar k'asa! kwanakin da suka wuce na dauka tare da kai muke jajanta yanda al'amura suke faruwa. rashin tsaro ha'inci da  cin hanci!  ashe ta ciki na ciki zuciyarka babu alkairi! akan miliyan talatin ka yarda kaci amanar Allah  har ka bada goyon baya kashe rai! shin ka dauka kai cewa zaka zauna a duniya ba zaka mutu ba?  haba Malam yanzu kana maganar kaddara! akwai ta amma kuma son zuciya yafi yawa a ciki saboda haka dole ka fuskanci hukunci daga hukuma!

A raunane! yace." Asp na amince da kowane irin hukuncin da za'a yanke a kaina!  kamar yanda na sheda muku da farko wallahi ba halina bane tsautsayi da kadd.........Umaru ya katseshi ta hanyar buga masa tsawa. "Ya isa haka."! shuru yayi yana kallonsa.
Ya kalli jami'an tsaron dake tsaye a kansa umarni ya basu cewa a fita dashi.
Suka mikar dashi tsaye.  damar da 'yan jaridar suka samu kenan suka dinga daukar hotonsa suna masa vedio sai sunkuyar da kansa yake abin duniya ya dameshi! basu fasa d'aukar hotonsa ba har sai  dai aka shige dashi mota tukkuna.

Kaf ya tattara bayanai da hujjoji da suka cancanta! da kansa ya kira kakakin rundunar 'yan sandan jahar! domin su sake tattaunawa, dama kuma  shine ya bashi wu'ka da nama domin yin binkice akan al'amarin.  bai jirayi komai ba ya had'a komai  kai tsaye kotu aka shiga dashi.

Mummunan labarin da ya faru a garin Katsina  shine Commissioner yayi mummunan accident a hanyarsa ta tserewa! yanzu haka dai yana kwance a asibiti rai a hannun Allah.  amma kuma cikin ikon Allah an samu nasarar kama Alhaji Mutari mai zinare yana hannu ana gudanar da binkice a kansa.

*Allah kayi mana tsari kasa mufi karfin zuciyarmu!*

To sai da 'kura ta lafa tukkuna! iyalinsu suka samu damar zuwa dubasu.

Lokacin Asp ya warware sai abinda ba za'a rasa ba, amma fuskarsa duk ta fitar da tabo in da Allah ya taimaka ma idonsa bai nakasa ba!

Kowa ya ke'be da iyalinsa  domin jajantawa juna. babban farin cikinsu ganin mazajen nasu sun samu sauki tare da samun nasara akan aikinsu. hakan ya faranta musu rai mutuka.

Ita da Hamra'u suka zauna a gefe da gefensa ma'ana suka sanya shi a tsakiyarsu.
Ita kam Uwale tana gefe zaune kan wata kujera.

Hankalinsa kaf yana kanta tausayinta duk ya dameshi  gabadaya kammaninta sun sauya sakamakon tsufan da cikin jikinta yayi.

Ya kamo hannunta ya rike cikin nashi. a tausashe! yace." Kiyi hakuri kinji ko."

Murmushi tayi kafin tace." Me akayi."?

Ya sauke sanyayyar ajiyar zuciya da fadin." A halin da kike ciki a yanzu ya kamata ace ina kusa dake amma hakan bai samu ba, sai rashin kwanciyar hankalin da ya faru! amma insha Allah komai zai wuce da ikon Allah."

Murmushin dai tayi don ta kwantar masa da hankali tace......

 *Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[5/21, 7:53 PM] Matar 'Dan Aljannah: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*124*
"A halin da ake ciki yanzu bana tare da damuwa ko wata fargaba! dalili kuwa nasan cewa duk

wanda ya dogara ga Allah tabbas zai tsaya masa, ma'kiya sunyi nufin ganin bayanka Allah bai nufa ba, gaka nan a raye kana cigaba da samun nasara a kansu hakika Allah yana tare da kai da duk wani mai gaskiya da zuciyar imani! ina cikin farin ciki sakamakon ganinka da rai da lafiyarka, kuma zan cigaba da yi maka addu'a Allah ya tsareka a duk in da zaka shiga Allah kuma ya d'aukaka darajarka duk wanda ke san ganin bayanka Allah yayi maganinsu."

Tun sanda ta fara maganar yake kallonta gabad'aya farin ciki mara misaltuwa ya Dabaibayeshi yau ya tabbatar da cewar yarinyar na 'kaunarsa tunda ga zahiri nan, duk mutumin da zai damu da kai ya kula da kai a lokacin da wata masifa ta sameka lallai babu shakka baka da masoyi sama dashi.

kawai ya cigaba  da murza hannunta dake cikin nashi, tsabar farin ciki ya ha nashi cewa komai ya kawai tsura mata rikirkitattun idanuwansa wanda suke kassara mata gabban jiki.

Kunyar abinda yake takeji gefe guda kuma tausayin Hamra'u duk ya dabaibaye ta.

Ta kalleshi tana nuna masa ita da ido.

Tana zaune tsuru duk ta muzanta. ta rasa ina zata jefa rayuwarta.

A hankali ya juya ya kalleta. shima kunyar ya d'an ji amma da yake namiji ne sai ya waske ya janyota jikinsa harda rungumeta.

Hakan ya faranta mata rai mutuk'a!

Itama Zinat din taji dadin abinda yayi.

A sanyaye tace." Yayana ya jikin? Allah ya tsare ya kiyaye gaba.

Cikin kulawa ya amsa da "Ameen ya Allah na gode sosai Allah yayi muku albarka."

Gabadaya suka amsa da "Ameen.

Uwale dake can gefe a zaune tana kallonsu tace " Wato Umaru idonka ya rufe baka tunani na ko."?

Murmushin yayi da fadin." Uwale ke gaisuwarmu dake ta daban ce, kece uwargida fa da tsohuwar zuma ake magani.

Tace." Ban yarda ba Umaru ni kam ina kishi da hakan."

Dariya yayi da fadin." Ashe baki yarda da maganata ba, Uwale kafin na samu kowa ke na samu saboda haka kada kiyi kishi ki kwantar da hankalinki."

Ta'be bakinta tayi ta mike tana kallonsu tace." Ku tashi muje duba abokin mijin naku idan kun gama soyayyar."

Hamra'u ta rufe baki da fadin." Uwale soyayya kuma."?

Tace." Kwarai kuwa ai duk naga abinda kuke kunsa shi a tsakiya kowacce tana kwarkwasa."

Zinat maganar ta bata dariya da mamaki! wai soyayya! mutumin da bai da ishashshiyar lafiya. koda yake shi din ma da zai samu faraga abinda zai aikata sai yafi haka.

To a takaice dai sai bayan la'asar suka fara shirin tafiya gida.

Mutumin ya wani lanjare wai shi lallai ba zasu tafi gabadaya ba dole wata ta zauna a cikinsu.

Uwale tace." Nasan wacce kake hari a cikinsu ka duba da kyau bata da lafiya cikinta ya tsufa ko ta zauna babu abunda za tayi maka.

Shuru yayi yana nazarin maganar.

Zinat din tace." Babu komai ke Hamra'u ki zauna tare dashi Aunty Zeey ma tana tare da Asp sai ku zauna a tare."

Hamra'u farin ciki ya cika mata zuciya, amma ta barshi a ranta bata fito dashi ba fili ba.

Uwale tace ." Hakan shine maslaha." Bai iya cewa komai ba tunda a zuciyarsa ba haka yaso ba.

Yaso ya samu sararin da zai rage zafi da ita amma hakan bai samu ba, tsabar idon Uwale da Hamra'u yasa ya hakura ya danne zulamarsa  da turtsetsan cikin ma sha'awa take bashi.

Bayan tafiyarsu Asp ya dinga tsokanarsa da cewa lallai kada yayi wasa tunda ya samu dama kawai yaci amarcinsa a asibiti yanda ransa yake so.

A zuciyarsa sam! bai sa abun a ransa ba, wacce yake kulafuci daban da wacce take gabansa, itama macace amma gabadaya hankalinsa baya kanta.

Tare da Aunt Zeey suka shiga kasuwar garin sukayi saye-sayen da za su bukata na yau da gobe.

Kowacce tana kula da mijinta dai-dai gwargwado amma dai babu wata shakuwar kirki a tsakaninsu gaisuwa ce kawai take had'asu kowa yayi sabgar gabanshi.

Sati guda suna tare su kwana su tashi guri guda amma bai ta'ba yunkurin yin wata mu'amula da ita ba.

Cikin dare yayi mafarki gashi yana sex. koda ya tashi duk jikinsa a 'bace. Ga joystick dinshi ta girma ta cika wando gabadaya yanayinsa ya sauya.

Da Asubah ya samu da kyar yayi sallah yayi zaune saman dadduma yana nazarin yanda zai bullowa al'amarin.

Ta fito daga bandaki daure da alwala kusa dashi ta tsaya domin gabatar da sallar......Tana idarwa ya kalleta da fadin "Zan kwanta yanzu kizo ki min tausa.

Ta amsa da " To." ba tare da ta cire hijab din jikinta ba tabi bayansa.

Ya tsira mata ido a lokacin da take tattaba jikinsa.

Sunanta ya kira, ta amsa tana kallonsa.

Yace." Kin shirya amsar sa'kona."?

Tace." Wane irin sako Yayana."?

Ya janyota jikinsa cikin kunne ya rada mata maganar.

Kunya ta ha nata cewa komai.

Shi kam jinta a jikinsa ya kara tayar masa da hankali. jikinsa ya dinga karkarwa! ya fara kokarin cire mata kayan jikinta.

Bata ha nashi hakkinsa ba, sai dai taci wuya a hannunsa ta raina wayonta taci kuka jin yanda yake sarrafata gabadaya ya kasa samun satisfaction saboda rashin wadatacciyar ni'ima taji ciwo sosai shima hakan.

Har gari ya waye suna abu daya.
Asp ya gaji da buga musu kofa ya tafi yana tunanin wani abu.

Kamar zautacce yake kiran sunanta da fadin." Ke din wace irin hallitace Hamra'u kin kasa gamsar dani kada ki jefeni cikin wani yanayi please ki taimaka min."

Murya a dushe tace." Yayana wane irin taimako zanyi maka bayan wannan nima na gaji ka taimaka ka sauka haka.

Ya girgiza kansa da fadin." Ba zan sauka ba sai na gamsu Zinatu ta fiki ta ko'ina ina alfahari da ni'imarta."
Maganar yake yana cigaba da bugunta duk a kokarinsa na ganin ya samu gamsuwar da yake bukata.

Kukan takaici kawai take cin zarafi da wulakancin yayi yawa yana tare da ita yana fadin kishiyarta ta fita ni'ima.

Bai damu da kukanta ba domin shi maganar ma bai san ya fada ba.....Da kyar da jibin goshi ya zubar da abinda ya d'aure masa mara, ya sauka jikinsa duk a kurje mussaman tsakankanin cinyoyinsa duk sunyi jaa! toilet ya nufa yana hada hanya kamar sabon dan kaciya.

Yana wanka yana tunanin al'amarin da ya faru tsakaninsa da yarinyar.

Ashe matan ma kala-kala ne, shi kam matarsa ta cika cif bai ta'ba samun matsala makamanciyar wannan da ita ba.

Hamra'u budurwa ce shi zai tabbatar da hakan, tinda ya kai minti ashirin yana artabu kafin ya ratsa jikinta, sai dai kuma a maimakon yaji yana nink'aya kamar yanda ya saba idan yana tare da Zinat sai kuma yaji bambaci gabadaya yarinyar a bushe take bata da dadi gashi duk taji masa ciwo.

Yayi wanka ya fito yana ya mutse fuska.

Magashiyan! a kwance ya sameta duk ta fice daga hayyacinta.

Tausayi ta bashi, yasa kayansa ya tsaya a kanta yana kiran sunanta.

Da kyar ta amsa amma bata tashi zaune ba.

Yace" Sannu kinji ko nima ba laifi bane amma kin san baki da lafiya ko."?

Makogwaro a bushe take kallonsa kafin tace." Ni Lafiyata lau ."

Ya gyada kai yana kallonta yace." Okey tunda kince haka shikkenan tashi ki gyara jikinki muci abinci kinji ana buga mana kofa ko."

Shuru tayi ba tace komai ba.

Wayarsa ya dauka ya kama hanyar fita.

Ta tsayar dashi ta hanyar kiran sunansa.

Ya tsaya ba tare da ya amsa ba.

A sanyaye tace." Ba zan iya tashi ba."

Yayi jim yana kallonta kafin ya isa gurinta.

Ya kamo hannunta ta sauke kafafunta kasa sai cije baki take.

Daukarta yayi ya nufi toilet din da ita.

Ruwan dumi ya hada mata yasa ta a ciki kafin ya fita ya bata gurin ta gyara jikinta.

Asp yayi ta tsokanarsa yana zolayarsa shi dai bai iya cewa komai ba saboda matarsa dake zaune a gurun.

A dakin yaci abincinsa ya koshi kafin ya nemi alfarmar Zeey din taje ta duba jikin Hamra'un.

Abinci ta had'a mata ta tafi mata dashi.

Bayan fitarta daga dakin ya kalleshi da fadin." Asp zaman asibitin nan ya isheni kunyi maganar da Dr Salihu ne."?

Yace." Eh dazu da ya shigo yake tabbatar min da cewar a cikin satin nan dai komai zai daidaita mybe ranar monday mu wayi gari a gida."

Ajiyar zuciya ya sauke tabbas zai so hakan domin ya gaji da zama guri guda ga masifar sha'awar matarsa dake damunsa.

Asp ya kalleshi da fadin." Ango na amarya."

'Karamin tsaki yaja da fadin." Asp mata dama iri-iri ne yarinyar nan fa ta wahalar dani."

Yace." Eh kowacce da irin baiwar da Allah yayi mata wata tafi wata haka abun yake.

Ya girgiza kansa da fadin." Ni zan sheda hakan."

Yace." Amma kada ka nuna musu a zahiri cewa ke nafi samun nutsuwa dake idan ka kuskura ka nuna hakan za samu matsala kayi kokarin boyewa."

Yace." Kasan Allah ban samu nutsuwa da yarinyar nan ba sai da na halarto Zinatu a cikin zuciyata tukkuna na samu satisfied  bayan haka kuma gabadaya duk jikina ciwo ne."

Yace." Ikon Allah amma meya janyo hakan."?

Yace." Sosai na sameta cikakkiyar budurwa amma babu ni'ima a bushe take k'amas!

Shuru yayi yana jajantawa abokin nasa.  yace." Kada ka damu ka fito fili ka fada mata yanayinta zata nemi magani kasan mace bata so ta zama koma baya mutukar su biyu ne ko uku ko hudu a gurin namiji.

Yace." Abinda nake tunanin yi mata kenan domin ba zan iya kayan haushi ba."

Asp murmushi kawai yayi kafin ya cigaba da bashi shawarwarin yanda zai samu zaman lafiya da iyalinsa.

Tun ranar da al'amarin ya faru bai sake takarta ba gudun abunda ka iya zuwa ya dawo. itama bata damu ba jinyyar kanta kawai take  domin ba k'aramin ciwo yaji mata ba.

Ranar da zasu tafi gida kam yafi kowa farin ciki ya bayyana a fuskarsa, sai walwala yake yana sallama da mutane cikin mutunci da karrama juna. kyautukan da ya samu a garin Zamfara baza su lissafu ba manya 'yan kasuwa da masu mu'kami 'yan siyasa da sauransu sun karramashi a ranar asibitin cika yayi domin yin bankwana dashi  da Abokinsa, abin alfahari ne ace ga ka gashi a hoto da yawa wasu sai da sukayi hotuna dashi irin na tarihi.
Daga gidan gomnatin garin aka dau'kesu a mota domin isa dasu muhallinsu.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*

*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[5/21, 7:53 PM] Matar 'Dan Aljannah: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*125*
To abinka da mai tsohon ciki tayi murna da dawowarsa gida, sai dai sam bai samu kyakykyawar kulawar da yake bukata ba, shi kuma idonsa ya rufe sai ya kasa yi mata uzuri! ya tsiri fushi da ita dan a ganinsa kamar ba tayi murna da farin cikin dawowarsa gida ba.

Shi yake abunsa domin a nata 'bangaran abinda ya dameta rabuwa da cikin jikinta lafiya! dan akan ga'ba take yau da lafiya gobe babu.

Washe garin ranar da ya dawo gidan, kasa hakuri yayi ya nemi hakkinsa nan fa d'aya! ita a lokacin ma mararta ke mata wani irin ciwo tana kwance lamo a kan gado yake kokarin turmusheta!

Kuka tasa masa tana tureshi da fadin." Baka da imani wallahi wai shin baka duba halin da nake ciki kake kokarin turmusheni."

Ransa ya 'baci jin abinda take fadi. yace." Ke baki ji kunyar fadin wannan maganar ba."?

Zaune ta tashi tana yin wani irin nishi tace." Wane irin kunya kuma gaskiya ce ai bani kadai ce matarka ba kayi min uzuri kuma tun jiya nace maka na amince kaje gurin Hamra'u babu komai wallahi."

Ya fusata! da fadin." Bana bukatar nata ke nake bukata akan me zaki hana ni hakkina baki da hujjar ha nani hakkina.''

Hannu tasa ta goge fuskarta da fadin." Wallahi bana jin dadin jikina babu wani abu da zan iya a yanzu kayi hakuri kawai.''

Ya tsira mata jajayen idonsa dake buge da muguwar sha'awa! jikinsa sai wani irin rawa yake.

Ya kad'a kansa rai a baci ya sauka daga gadon  ya dauki rigarsa yana kokarinsa sanyawa a jikinsa.

Kallonsa kawai take tana mamakin tsabar fitinarsa  in banda abinsa Hamra'un ma ai macace kuma da amincewarta ta yarje masa yaje gurinta amma ya kasa fahimtarta ita kam ba zata iya da fitinarsa ba.

Saboda babu yanda zai yi haka ya hakura yaje gurin Hamra'un da bukatarsa.

Sai dai itama kafin ta amince masa sai da sukayi artabu! dan har yanzu bata mance ba'kar wuyar da tasha a hannunsa ba.

Takaicin abinda take masa yasa ya rufe ido yaci mutuncinta iya son ransa! yace." Nima dole tasa nazo gurinki da har kike min rashin kunya! had'uwata dake da farko nasha wuya saboda haka inaso na sheda miki cewa lallai ki nemi magani domin baki da ni'ima ko kadan."

Ta dinga kuka kamar ta hadiyi zuciya ta mutu saboda bakin ciki!

Bai damu ba ya danneta yana rawar jiki da adduar Allah yasa yaji dai-dai! inaaa! ai babu wani sauyi domin jiya i yau!  cikin salo da 'kwarewa yake mata wassanni ko za'a samu cigaba babu wani bayani watakila dai haka hallitar take.
Yaja tsaki babu adadi! gumi duk yayi masa dabaibaiyi  ita kam jin wuya tayi wuya! gabanta duk ya tsage yana radadi! kawai ta  bud:e murya ta dinga kurma! ihu! tana rokonsa ya sauka haka.

Kamar mayen karfe ya nane a jikinta yaki rabuwa da ita. hawayen takaici da bakin ciki suke kokarin subce masa, idan ya sauka bai gamsu ba zai iya mutuwa! shiyasa yake ta kokarin ganin ya biya bukatarsa!

Uwale dake cikin daki ta dinga jin ihun! hankali a tashe ta fito kai tsaye dakin Hamra'un ta nufa tana bugawa domin ba ta tsammaci cewa yana ciki ba tunda lokacin daya shigo tana d'akinta domin gabatar da salhar walha.

Fadi take "Hamra'u lafiya shin  me  yake faruwa ne? ki bude kofar mana."

Jin muryar Uwalen yasa da sauri ya rufe mata baki da  tafin hannunsa! bai saurara mata ba har sai da ya zubar da abinda yake mararsa a galabaice ya zube kan gadon yana janyo numfashi

da kyar!

Yafi minti ashirin a kwance yana nishin wahala bacci ne yake kokarin d'aukeshi! bugun kofar Uwale yasa firgit ya tashi!
Ya harari gurin da take kwance, bece mata komai ya tashi yasa kayansa, ya tsaftacce jikinsa a d'akinsa.

Yana fitowa suka bishi da kallo. Ita Zinat ba tayi mamaki! ba Uwale ce dai take masa kallon mamaki!

Da sauri ya ratse su ya wuce ya barsu da binsa da kallo.

Uwale ta girgiza kai har yanzu da mamaki a tare da ita, koda yake babu mamaki ai mutumin yau ne abinda yafi haka ma zai aikata.

Kai tsaye dakin ta shiga Zinat din ta rufa mata baya.

Suka sameta a kwance babu yanda take tayi wuri-wuri!

Dukkaninsu sun d'auka yau ne ranar farko dan ganin yanda tayi wurjajan!

Uwale ta  tsaya kanta da fadin." Sannu da alama gardama ki kayi masa shine dalilin da ya sanya shi ya gwada miki karfi."!

Girgiza kanta tayi murya a dashe tace." Aa banyi masa gardama ba! da zafi yake min."

Zinat dariya ta kamata amma ta danne ba tayi ba  kawai tayi shuru tana kallonta.

Da kyar Uwale ta taimaka mata suka shiga bandaki a tare.

Ta fita daga dakin tana danne wani abu dake taso mata a can kasan zuciyarta.

Sai dai tana shiga dakinta ta sameshi a kwance saman gadonta daga shi sai gajeran wando ya bude kafafunsa.

Ranta ya 'baci! ganinsa to meye amfanin hakan da yayi?

Ta hade fuska da fadin." Meye haka."?

Ido a lumshe yace." Bani da lafiya zo ki dubani."

Taji kamar ta rufeshi da duka! yaje ya gama more rayuwarsa zai zo ya kwanta mata a gado!

Ta juya zata fita  cike da takaicinsa.

Sunanta ya kira, taja ta tsaya tana watsa masa harara!

Zaune ya tashi ya kira ta da hannu wai tazo gurinsa.

Zumbura baki tayi da fadin." Me zanyi maka kuma."?

Yace." Ke dai kizo kiji wata magana."

Ajiyar zuciya ta sauke ta isa gurin amma bata saki fuskarta ba.

Ya zaunar da ita kusa dashi! kawai ya fara kokarin cire gajeran wandon jikinsa!

Gabanta ya fadi! da sauri tayi yun'kurin barin gurin ya rike hannunta da kyau!

"Ba wani abu zan miki ba zan nuna miki ciwon da naji."

Ta dinga kallon tsabar rashin kunyar da namiji.

Kauda kanta tayi  ba wai yau ta fara ganin girmansa ba kawai dai tana jin nauyi saboda akwai haske a garin.

Ya juyo fuskarta yana marairaice fuska yace." Duk da Asp ya gargadeni kan cewa kada nayi wani furuci akan al'amarin a wannan ga'bar dole nayi magana dalili har yanzu ban samu abunda nakeso ba sai 'bakar wuya da nake sha. Zinatu ki duba kiga irin  raunin dana samu sakamakon had'uwata da Hamra'u."

Da sauri ta kalli gurin gabanta na wani irin faduwa!  kan  duk ya dad'e yayi jawur! hakan nan tsakankanin cinyoyinsa sunyi jawur!

Cike da mamaki take kallonsa  kafin ta iya fadin." Me ya janyo hakan."?

Yana kokarin mayar da wandon yace." Bata da lafiya na fada mata amma ta musanta saboda haka daga yau ba zan 'kara kai kaina halaka ba."

Maganar ta bata dariya yanda ya fada da gaske yake sai cin magani yake kamar wanda akayi wa gagarimin laifi.

Sai da ta dara tukkuna tace." Aa ai ba za'ayi haka ba rashin sabo ne kawai haka zaka daure har ku saba da juna."

Yaja dogon tsaki da fadin." Ba zanyi ba! na fada miki domin idan nace lallai sai nayi to watarana zata nakastani domin daga ranar da akace babu wannan abar kema ba zaki zauna dani ba."

Ta fashe da dariyar da take dannewa! ta dinga kallonsa tana mamakin al'amarin!

Cikin tsare gira yace."Kin raina ni ko? ina magana kina min dariya."

Ta sassauta da fadin." Ai abun ne da ban dariya wallahi!  to yanzu wace shawara ka yanke."?

Yace." Wacce na fada miki yanzu."

Ta sauke ajiyar zuciya da fadin." Ni kuma ina tunanin rashin ni'ima ne ai cikakkiyar budurwa ce ko."?

Kansa ya gyada alamar Eh hakane.

Tace." Kada ka damu ni zan taimaka muku."

Ya kalleta da mamakin furuncinta. shin wane irin taimako za tayi masa. shifa ba zai iya ba  dan ya gaji.

Hannunsa ta rike da fadin." Ka daina tunani insha Allah zan bada gudumawata yarinyar ta bani tausayi."

Yace." Ke kinga nifa ba zan sake komawa ba kawai dai kiyi hakuri duk sanda bukata ta kawo ni gurinki ki amince min."

Tace." Nima kayi hakuri kayi min uzuri my love."

Ya kalleta wani sonta na k'ara tsirga mishi.

Tace." Idan na haihuwa zan baka kulawa irin wacce ba kayi tsammani ba."

Ya lumshe idonsa da fadin." Ko wane yanayi kike ciki  ina kaunarki ina alfahari dake kin riga kin zama wani sashe na jikina.
Murmushi tayi ta sake rintse hannunsa dake cikin nata. "Na gode Allah ya barmu tare." Ya amsa da "Ameen tare da rungumeta a jikinsa.

To kamar yanda tayi alkawarin bada gudumarwata akan al'amarin.
Ta taka muhimiyyar rawa domin magungunan mata irin na tayar da sha'awa da karin ni'ima wanda *BINTA UMAR ABBALE  ke siyarwa  masu kyau da inganci ta d'auka! gabadaya ta kai mata sannan tayi mata bayanin yanda za tayi amfani dasu.....Ingantattun Magungunan hausa ne irin na islamic wanda aka tantance babu cuta babu cutarwa! sai wanda ya gwada zai tabbatar da ingancinsu.*

To A ranar da ta fara amfani da maganin taga sauyi a jikinta  sai da ta sauya pant sau uku bayan haka ta dinga jin wani irin feeling a tattare da ita. Hamra'u dai haka ta yini tana matse cinyoyinta.
Saboda yanayin da ta shiga ya rikirtata bata bukatar kowa sai mijinta.

_Akwai ingantattun magungunan hausa da aka tantance masu kyau! ga duk mai bukata sai yayi magana....07084653262_

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[5/21, 7:53 PM] Matar 'Dan Aljannah: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

_Team d'in Zinatu naga comment's dinku 😃 kuna yin kishi saboda Zinatu ta taimaki Hamra'u da maganin mata! bahaushe fa yace ciwon ya mace na ya mace ne🙈Kishiya kuma 'yar uwa ce mutukar zama yayi dadi_

*126*
To da sauki-sauki za'a ce  bai sha wahala ba a lokacin da yayi tarayya da Hamra'un, sosai yayi mamakin al'amarin ya kuma sanya a ransa cewa matarsa na daga cikin jerin salihan mata nagari! yasan cewa abinda tayi ba kowace mace zata iya ba,  yaji dadi sosai kuma ta kara matsayi da girma a idonsa.

Haka ya dimanci Hamra'u babu dare babu rana. mutukar yana gida  to tana cikin fargaba! kalankasa ce sam bata da juria shi kuma abun   haushi yake bashi adduarsa kullum shine Allah ya sauki matarsa lafiya.

Rabo idan ya rantse babu yanda za'ayi  Hamra'u ta dauki ciki sati guda kowa ya fahimta domin mai bala'in laulayi ne.

Ta lanjare! ta gaza tabuka komai kullum tana kwance tana juyi ga zubda yawu da amai duk ta figale!

Gabadaya ta fice masa daga rai! ya daina sha'awarta saboda yawun da take tarawa a bakinta ga rashin wanka da tsabtar jiki, saboda cikin da suddabaru yazo mata sam bata san zubawa jikinta ruwa.

A lokacin kuma shi sai Allah ya jarabce shi da fitina da rashin hakuri! ga matayen nasa duk babu cikakkiyar lafiya.

A wani dare ya zunguro mata nakuda!

Domin gurfana yayi a gabanta yana rawar murya kan ta barshi yayi ko sau daya ne.

Tausayi ya bata  ganin abinda yake kamar wani zautacce!

Ashe jira yake ta bashi dama yana samu ya fara sukuwa a kanta shaf ya manta da lalurar dake tare da ita.

Ta galabaita sosai! tana rokonsa ya bari haka.

A lokacin yake jin wani karfi ji yake kamar ranar suka fara had'uwa! wasu hawaye suka dinga sulmiyowa daga idonsa ya gaza tsayar dasu shi ya san ko na meye.

Ya samu satisfied amma a maimakon ya sauka kokari yake ya cigaba dan joystick din taki rusina tana nan a tsaye alamun dai bata gaji ba.

A galabaice tace." Idan ba kasheni kakeso kayi ba dan zatin Allah ka bari haka wallahi dab nake na haihu domin ni ka dai nasan abinda nakeji."

Jikinsa yay sanyi jin abinda tace.

Ya kama fuskarta ya dinga sumbata yana shan bakinta kamar ba zai bari ba.

Da kyar ya bawa kansa hakuri ya kuma yi kokarin kwantar da zulamarsa ya sauka daga kanta ba dan ransa yaso ba.

Toilet ya nufa yana jin wani irin farin ciki a tare dashi.

Da kyar ta iya wanka tazo fitowa daga toilet din kafa ta rike ta gagara takuwa!

Ta rintse ido tana kiran sunan Allah!

Duk ya rasa yanda zaiyi ya riketa yana tambayar abinda ke damunta.

Can kasan makoshi tace." Haihuwa zanyi ciwon yafi na kullum.

Hannu na rawa ya fito da waya ya fara neman Asp domin ya turo masa Madam su shirya zuwa asibiti.

To kafin ma Madam din ta shigo faya ta fashe.

Jin abu na dannowa yasa ta zube a gurin tana wani irin nufarfashi!

Ya riketa sosai a jikinsa yana mata sannu gabadaya tausayinta ya rufeshi.

Madam ta shigo taga halin da ake ciki. kallo daya tayi mata ta gane cewa akan ga'ba take.

Tayi-tayi dashi ya fita amma fir yaki yace lallai a hannunsa zata haihu.

Hakan nan ta kyaleshi ta  gyara gurin ta shimfida wata leda sannan ta umarceshi daya kwantar

da ita akai.

A kan cinyarsa ya kwantar da ita ya zauna sosai saman ledar kamar shi zai haihu.

Nishin da kansa yake zuwa ta dinga tana kiran sunan Allah Madam din na taimaka mata. shi kuma sai karkawa jikinsa yake gumi duk yay masa dabaibaiyi wannan tashin hankali har ina! ashe haka mahaifiyarsa tasha gumurzu! kafin ta haifeshi! yaji wasu zafafan hawaye suna kokarin kwace masa.

Yana can yana zulumi da rawar jiki ta haihu! kukan baby ya dawo dashi hayyacinsa!

Ya rintse idonsa yana kiran sunan Allah.

"Alhamdulillahi-Alhamdulillhi-Alhamdullahi."

Sai da ya fadi haka sau uku sannan ya bud'e idonsa.

Lokacin Madam ta daga yaron tana d'aure masa cibiya bayan ta yanke.

Duk da ya fahimci abinda ya samu sai da ya tambayeta.

Tace." Eh namiji ne gashinan tubarkalla kamar kayi kaki ka tofar."

Murmushi yayi yana sake godewa Allah a cikin ransa.

Sai da maijego da babyn sukayi tsaf sannan su Uwale suka ji labari.

Irin wannan haihuwar tana da dad'i! Uwale bakinta kamar gonar audiga godiya kawai take ga Allah.

Hamra'u kadaran kadahan!  amma a zahiri ta nuna farin cikinta, sai dai kuma babu wanda ya san zuciyar mutum sai Allah.

Ganin yanda yake ta murna da kai kawo ya sanya itama take adduar Allah ya sauketa lafiya

domin taga irin farin cikin da zai yi.

Kwana uku da haihuwar yayi wa yaron huduba da sunan abokinsa Asp *MUSA* kenan.

Uwale tace ya cancanta hakan kuma yayi dai-dai.

Asp ya gaza boye farin cikinsa yayi ta godiya akwati uku ya ciko da kaya masu tsada na maijego da takwaransa.

Wannan haihuwa ta janyo alkairai masu yawa! domin wani irin kyautuka ya dinga samu daga manya manyan mutane! maijego ita kanta ta samu alkairai masu yawa daga gurin abokan aikinsa da sauran masoyansa.

A kayi shagalin suna mai kayatarwa.
'Yan jarida masu neman labarai suka abin yayatawa a gari.

Hamra'u dai daki ta shiga taci kukanta ta koshi! gani take kamar ma yanzu babu mai kaunarta.

Mutanan *Kafur!* din ma da suke nuna mata kauna daso yanzu gabadaya sun manta da ita. alherin da Zinat din take musu yasa sun mayar da hankalinsu gurinta, suyi tayi mata fadanci da kirari! ita kuma tana musu kyautuka na bajinta. duk yawansu da suka zo bikin sunan sai da suka samu alkairi daga gurinta suka tafi cike walwala da farin ciki tare da alkairai masu yawan gaske.

'Dayyiba ta sake bazama! neman asiri wannan karan babu sassauci! ta kudiri mummunar aniya!

Ta taki nasara samo zazzafar asiri sai dai kuma yana da had'ari tace taji ta gani zata iya.

Sai dai cikin ikon Allah kafin ta isa gida Allah ya mantar da ita sharud'an daka a gindaya mata.

Ta firgita sosai! sai ta juya domin komawa gurin bokan.

Kafin ma ta isa bukkar taji ana katantanwa! da ita ba'a ajiyeta a ko'ina ba sai a kofar gidanta!

Baki a murgude kafa da hannaye a shanye!  anan gurin kudaje sukayi mata dabaibaiye yawu na dulala a bakinta.

Cikin tashin hankali aka shiga da ita gida ana mamakin al'amarin.

Labari ya samu Hamra'u ta dinga kuka ta rikice musu lallai sai taje ta duba mahaifiyarta.

Dama yana jin haushinsu yace babu in da za taje.
Ya riga ya yanke hukunci duk wanda ya sa baki sai ransa ya 'baci!

Zinat ganin abinda yake bai dace ba, ta bullo masa ta bayan gida.

Suka dinga sa'insa! a tsakaninsu shi yana nuna mata ikonsa ita kuma tana nuna masa rashin dacewar abinda yake, iyaye sun wuce wasa.

Ya fusata!  yace." Idan ke kike da iko sai ki bata izini taje."
Ya buge rigarsa ya fita daga gidan.

Sai kawai ta yanke shawarar  shedawa Asp halin da ake ciki.

Shima ransa ya 'baci sosai.

Yace." Suyi hakuri zai magana dashi.

To da kyar ya shawo kansa har ya amince.

Ya dinga jin haushi koda ya dawo gidan sabgar gabansa yake bai saurari kowa ba itama bata kulashi saboda ta san duk rintsi ba zai kwanta ba sai ya duba yaronsa.

Aikuwa wajen sha daya na dare ya shiga dakin.

Cikin alamun bacci ta tashi zaune tana kallonsa.

Yace." Kin fara bacci ne."?

A dakile ta amsa.

Ya sauke ajiyar zuciya da fadin." Ya jikin abokina  ina fatan zazzabin ya sauka."

Tace." Eh yanzu dai babu baccinsa yake tun dazu.

Ya kunna wayarsa yana dubashi.
Yaron yayi wayo sosai watanshi hudu yanzu kamar dan wata bakwai.

Yace." Gobe zaku shirya zuwa *Kafur!* amma a ranar zaku dawo dukkanku."

Tace." Har ita Hamra'un."?

Yace." Eh har ita domin zamanta a garin sam bai da amfani."

Cike da mamaki take kallonsa kafin tace." Ya asalin bashi da amfani bayan iyayenta da duk 'yan uwanta suna garin.'

Yace." Mahafiyarta bata da kirki mutuniyar banza ce."

Ta dinga kallonsa da mamakin maganarsa.

Tace." Wai dan Allah me tayi maka ne ka tsaneta haka."?

Tsaki yaja da fadin." Ba lallai sai kinji ba amma bari na baki sako idan kun isa garin ki sheda mata cewa duk wanda ya shafeni yafi 'karfinta kuma duk abinda ta k'ulla yana dawowa kunnena."

Tace." Kai waye ya fada maka? dan Allah kada ya yarda da jita-jita na mutane.

Yace." Mutumin da ya tabbatar min da gaskiyar al'amarin mutumin arziki ne idan kina bukatar magana dashi sai na had'aku."

Tace." Ni ina ruwana dashi kuma! sai dai   kai daka yarda da maganarsa.

Ya buga mata tsawa! jikinsa na kyarma yace." Ki kiyaye bakinki. domin wannan bawan Allahn ya tsaya miki bayan sahalewar Ubangiji shima yana taka muhimmiyar rayuwa a rayuwarki da tuni kina kwance babu lafiya.

Ta dinga kallonsa tana mamakin maganganunsa. Wato aljanunsa ne suke sheda masa duk abinda yake faruwa.
To ita kam a duniya me tayi wanda mahaifiyar Hamra'u zata cutar da ita.

_Ba kiyi mata komai ba tsabar rashin tsoron Allah ne_

*Wanda suke bukatar ayi musu typing da Azimi su d'aga Hannu😜*

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[5/21, 7:53 PM] Matar 'Dan Aljannah: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*BARKANMU DA SALLAH 😊*

_*RAHMA IDRIS GA GORON SALLAH NAN🙏🏻😀*_

*127*
Da taimakon Zenat shirye-shiryen tafiya k'auyen *K'afur* ya kammala, sunyi tsaraba daidai gwargwado sai dai shi uban gayyar yace babu in da zashi a cewarsa yana da aiki a gabansa, Hamra'u kamar ta fashe da kuka saboda bacin rai! ta lura dashi ya dauki karan tsana ya dorawa mahaifiyarta ta rasa meye dalili, a fakaice ta dinga share hawaye, tausayinta ya rufe Zinat din, yana shirin fita ta sameshi a dakinsa domin ta nuna masa cewa abinda yake wa yarinyar bai dace ba, iyaye sunfi karfin wulakanci duk d:a nagari ba zai so yaga ana wulakanta iyayensa ba.

Tana ta magana yayi shuru bai ce komai shirya jikinsa kawai yake, ya zauna gefan gado yana daure igiyar takalminsa, tace." Magana nake da kai ka share ni abinda kake sam bai dace ba,

kuma rik'o bashi da amfani ka dai daure kaje ka duba jikin matar nan yanzu idan kuma rai yayi halinsa mai za ka kace."?

Ya kalleta babu sukuni a fuskarsa yace." Da zata mutu da yafi alkairi."

Gabanta na faduwa ta dinga kallonsa tana mamakin furuncinsa.

Tsaye ya mi'ke da wayoyinsa a hannunsa.

"Ni zan fita." ya fada babu wata damuwa a tare dashi.

Ta mike da fadin." Gaskiya ka sauya halinka dan wallahi abinda kakewa yarinyar nan ba daidai bane."

Ya fusata! ya nunata da tsaya da fadin." Wai shin ke kike auranta ne ko kuwa? kada fa kiyi min rashin kunya dan zan 'bata miki rai nace ban zanje ba da duk abinda za'ayi aje ayi."

Ganin yanda yake magana a hasale! yasa ba ta sake cewa komai ba ta fice daga d'akin ranta a masifar 'bace.

***

Yanayin halin da suka samu 'Dayyiba ya firgitasu, gabad'aya kammaninta sun jirkice ta rame tayi ba'ki'kirin ba ta san ma wanda yake kanta ba. Hamra'u dai fashewa tayi da kuka tana kiran innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! wane irin ciwo ne wannan.

Gaje 'yar uwa ce ga Dayyiba itace kuma take jinyarta, nan take sheda musu cewa an kaita asibiti amma har yanzu an kasa gano abinda ke damunta ganin haka yasa suka dawo gida suke na hausa.

Ta jima tana jajanta al'amarin kafin ta sauke zazzafar ajiyar zuciya, tasa hannu ta goge hawaye daya sakko a saman fuskarta, ido ta tsira mata, tana kwance kamar jikakken tsumma! sai gwalantu take yawu da majina na dulala, k'udaje na bin jikinta 'Yar uwarta na kore mata da mafici.

A sanyaye tace." Allah ya sawwa'ke amma wane irin asibiti ku ka kaita."?

Tace." Na gwamnati ne."

Ta girgiza kai da fadin." Ba wai na raina na gwamanatin ba, idan babu damuwa yanzu a shirya ta sai mu kaita na kudi   idan kun amince insha Allah zanyi komai."

Gaje ta share hawaye da fadin." Wallahi da har mun hakura domin munfi gazgata cewa wannan ciwon ba na asibiti bane amma ba za muqi  ba, bari Mijinta ya shigo sai a sheda masa.

Tace." To shikkenan babu damuwa.

Uwale da tunda suke maganar ba tace komai ba sai yanzu  tace." To Allah dai ya sawwake ya bata lafiya.

Gabadaya suka amsa da ameen."

Ta juya ta  kalli Hamra'u dake share hawaye tace."  kiyi hakuri addua zaki mata ki daina kuka da sanya damuwa a ranki insha Allah zan tsaya muku daga abinda ya sawwaka daga gareni.

Ta rike hannunta da fadin "Na gode sosai Allah ya saka miki da alkairi,  abinda nai miki ki yafe min."

Ta rungumeta da fadin." Baki min komai ba Hamra'u zaman tare ne, idan ma kinyi min na yafe miki Allah ya yafe mana baki daya."

Uwale da Gaje suka amsa da "Ameen cikin yanayi na alhini da damuwa.

To koda Malam Shafi'i yaji maganar bai yi jayayya ba, lokaci guda ya amince domin gabadayansu  hankalinsu ya tashi da al'amarin.

Babban asibiti suka nufa da ita, duk irin shige da ficen da ya kamata ayi  a kanta anyi a take a lokacin ta kar'bi account din asibitin ta turawa Magajin Sarki dan uwanta domin ya tura musu zunzurutun kudin da suka bukata kimanin dubu dari takwas da hamsin.

Shi kansa Magajin sarkin sai da ya jajanta al'amarin kuma ya tausayawa matar, saboda haka ba tare da bata lokaci ba, ya tura kudin, aikuwa manya likitoci suka tsaya a kanta domin bata taimakon gaggawa.

Sai da komai ya kammala sannan ita da Uwale sukayi musu sallama direba ya daukesu suka nufi masaukinsu, Uwale ta shiga hidimar dora abinci, ita kuwa  wanka tayi ta kwanta tana hutawa, amma fa har yanzu akwai fargaba da damuwa a tattare da ita,  tana da tsananin

tausayi shiyasa duk lokacin da ta tuna halin da mahaifiyar Hamra'u ke ciki sai hankalinta ya tashi.

Kiran wayarsa ne ya tayar da ita, da lalube ta janyo wayar tana dubawa.

kamar ta ajiye wayar domin har yanzu tana jin haushin tsawar da ya buga mata sai kace wata 'yar cikinsa

Ta dauki wayar tare da daidaita yanayin maganarta.

"Barka da yamma." shine ya gaisheta.

Ta amsa da fadin."Barkanmu dai ya aiki."?

Yace." Alhamdullhi fatan kun sauka lafiya."

A takaice tace."Lafiya lau."

Yace." Ina yaro na."? jim tayi kafin tace." Tun bayan zuwanmu Kawu Ado ya turo aka daukeshi yana dai can gidansa.

Yace." Naji dadin hakan.".

Shuru ya ratsa na second biyu, ta daure tace "Baka tambayi mai jiki ba."

Yace." Ai nayi ta kiran wayar Hamra'un bata dauka ba."

Murmushin takaici tayi kafin tace." To ta yaya zata daga wayarka bayan kana tsangwamarta ranar lahira za'a tuhumeka kada ka kira sunana dan wallahi ni ba zaka had'a baki dani ka cuci matarka ba."

"Allahu akbar malama sai ki fada min cutar da nayi mata, wai shin mai yasa kike kokarin dora min laifi ne."?

Shuru tayi masa takaicinsa duk ya isheta.

Yace." Bani Uwale mu gaisa domin ina da Uzuri."

Tace." Yawwa dama akwai maganar da zan fada maka."

Yace." Wace magana ce."?

Ta jima tana tunanin hanyar da zata bi gurin sheda masa halin da ake ciki, da kyar dai tayi shahada ta fara fada masa mawuyacin halin da suka iske mahaifiyar matar tasa a ciki da irin taimakon da tayi mata.

Ya gama saurara tsaf  har ta kammala, ya ja dogon tsaki da fadin." Wanene ya saki aikata hakan."?

Tace." Babu kowa tausayi ta bani wallahi har sai dana zubar mata da hawaye.

Yace." Zakiyi wani kukan domin wannan da ki kayi shafar mai ne, abinda nakeso dake yanzu shine maza  ku dauko matar nan daga asibiti domin lalurar dake damunta bana asibiti bane.

Shuru tai masa domin bata tsammanin aikata abinda ya umarce ta.

Yace." Ko ba kiji abinda nace ba."?

Jiki a sanyaye tace." Naji."

Ya kashe wayarsa ransa duk a 'bace! ya tsani kankanba! a lokacin da take shaida masa abinda ta aikata yaji a jikinsa cewa akwai abinda zai faru,  aikuwa a daran jikin Dayyiba ya rikice  wasu manya manya kuraje suka feso a jikinta! sunyi jawur!  sun d'uri ruwa sai kaikaiyi suke mata tana zumduma ihu!

Su kam likitocin babu wata damuwa a tare dasu suke gudanar da aikinsu, suka dinga zurkud'a mata karfe suna fashe k'urajen suna matse wani irin ruwa mai wari da kauri da jini babu kyawun gani.

Al'amarin ya tsananta sosai gabadaya jikin Dayyiba ya baibaiye da Kuraje babu masaka tsinke, dan koda suka isa asibitin suka iske halin da ake ciki sai da hankalinsu ya tashi.

Gaje na goge guntun hawayen fuskarta tace." Hajiya Zinatu kinga yanda abu ya dawo ko shiyasa nace wannan lalurar bana zuwa asibiti bane.

Jiki a masifar sanyaye tace." Nima naga alamar hakan saboda haka bari na samu likita muyi magana idan da yuwuwa a bamu sallama muje gida.

To shima likitan dai bai yi jayayya ba, domin ansha kawo masa marasa lafiya irin wannan, sukan yi iya bakin kokarinsu akai idan ya gagaresu kawai sallamar mutum suke tare da fadin aje a gwada na hausa.

Amma bai basu sallama a ranar ba yace. sai zuwa gobe tukkuna.

Aikuwa a daran rai yayi halinsa, Dayyiba ta amsa kiran ubangiji, INNALILLAHI WA'INA ILAIHI RAJI'UN!

Mutuwar tayi masifar girgizata ba kadan ba, ta dinga kiran sunan Allah a zucci a bayyane.

Gari ya kacame! da surutu! kace nace! kowa da abinda yake fada cewa kishiyar Hamra'u ce sanadiyar mutuwar Dayyiba.
Da yawa wasu sun yarda da hakan, amma wa'inda basu yarda ba sun fi rinyaje.

Ita dai uwar dakin Uwale ta shiga ta kwanta tana kuka, dama sai da mijinta ya gargad'e ta amma taki jin maganarsa.

Hawaye take sharewa tare da adduar Allah ya fitar da ita.

Har akayi jana'izar Dayyiba tana kwance a daki domin fargaba take taje gidan mutuwar saboda tana gudun abinda zai biyo bayan zuwan nata.

Koda ya samu labarin mutuwar matar bai damu ba, a ganinsa mutuwar itace tafi mata alkairi, koda taji sauki ta dawo gida wahala zata sha ayi ta fama da ita dan ba zasu ta'ba fahimtar me ya janyo faruwar hakan ba sakamako dai ya bayyana a yanzu alamu sun nuna cewa ta shiga hurumin babban aljanin da baya son wargi.

A daran ranar wani mugun zazzabi mai zafin gaske ya rufe ta, ta rufe jikinta a gado tana ta makyarkyata da faduwar gaba, ba komai ne ya janyo mata wannan zazzabin ba sai fargaba da tashin hankalin faruwar al'amarin da take ganin kamar itace silar faruwarsa.

*Kada ki karanta min littafi idan baki biya,  kada ki siya ki fita dashi, 'Yar uwa kada ki ganshi a group kiyi shearing domin hakkina ne, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne.....0542382124...Binta umar gtbank. idan kati zaki turo sai kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[5/21, 7:53 PM] Matar 'Dan Aljannah: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*128*

*(Rahma Idris) daughter (Zainab Khabir Ishak) da sauran magoya bayan wannan littafi na GOJE ina mai baku hakuri, hakikanin gaskiya na san dole ranku ya 'baci, na rashin samun Update kullum kamar yanda nayi alkawari, Kuyi hakuri nima ba sa'an raina ba,  haka Allah ya tsara min ina cikin jarabawarsa😭 a halin yanzu bani da nutsuwar typing, abubuwa da yawa sun dameni, wannan shine cikar mumuni, dole rayuwa ta tafi da jarabawa, muna rokon Allah ya jarabce mu da irin wacce za mu iya dauka🙏🏻*

*KUYI HAKURI KU SANYA NI CIKIN ADDUARKU😭🙏🏻*

Da zazzabi ta kwana ta tashi, jiki ram! duk ta fyade tayi wata irin rama ido yayi zuru-zuru!
Uwale hankalinta ya tashi, ita ta dinga dawainiya da ita kafin Umar din ya sauka a garin.
Ganin halin da take ciki ya sanya jikinsa sanyi,  ya umarce da ta shirya maza suje asibiti likita ya dubata, kafin ya dawo daga gidan mutuwar, domin yana so su kama hanyar gida a ranar.

Uwale tace." Daka bari ayi sadakar uku mana."

Kansa kawai ya girgiza ya sanya takalmansa ya fita da sauri.

Kai tsaye gidan mutuwar ya nufa.

Duk da yana jin haushin mai mutuwar sai da ya tausayawa iyalinta.  ya shiga har cikin gidan yayi musu gaisuwa, jama'a sukayi caa! a kansa, sai ya dinga jin kunya da nauyi abinda ya faru yasan da yawa daga ciki  akwai abinda suke tunani a kansa da matarsa.

Sai da ya fita daga gidan kana ya samu yaro ya umarceshi daya kira masa Hamra'un  sosai yarinyar ta bashi tausayi .

Ta fito ta sameshi yana waya.

tsayuwa tayi jikin bango( garu) tana kallonsa itama duk ta rame abinka da mai k'aramin ciki fargaba da laulayi sun sanyata a gaba.

Cikin kulawa ya kalleta da fadin." Ya karin hakuri."?

Wasu hawaye masu zafi suka kwace mata.

Ya girgiza kansa da fadin." Kiyi shuru ki daina kuka addua zaki cigaba dayi mata.

Ta share hawayen fuskarta tana sauke ajiyar zuciya.

Yace."  Jikin naki da sauki ko."?

Kanta kawai ta iya dagawa.

Minti biyu yana kallonta kafin yace." 'Yar uwarki ma babu lafiya sakamakon abinda ya faru  ina fata dai kinyi mata kyakykyawar fahimta akan lamarin.

Taja hanci kanta a sunkuye tace." Wallahi bana zargin aunty Zinat domin da kyakykyawar niyya a zuciyarta, kawai dai lokacinta ne yayi, suma mutanan dake zarginta dan basu san wacece ita bane.

Ya jima yana kallonta kafin yace." Naji dadin hakan sannan ina fatan suma sauran mutanan dake zarginta su gane gaskiya.

Shuru tayi ba tace komai ba.

Hannu yasa cikin aljihu ya dauko kudi da yawa ya bata da fadin ." Ayi sadaka insha Allah ranar adduar bakwai zan dawo sai mu tafi tare.

Tace." Zaku tafi ne yau."?

Kai ya daga yana duba agogon dake daure a hannunsa.

Jikinta duk ya mutu jin cewar zasu tafi.

Ya kalleta tare da d'an girgiza kansa hakurin dai ya sake bata kafin yayi mata sallama ya fice daga soran gidan.

A tsaitsaye ya gaisa da Kawunansa kafin ya isa gidan ta shirya tsaf tana zaune gefan gado tare da kokon fura da nono a hannunta, tunda tayi wanka da ruwan dumi taji sassauci.

Uwale dai cewa tayi sai ranar adduar bakwai idan yazo sai su tafi domin yanzu tana iya tafiya surutu ya biyo baya, abinka da kauye.

Sai da sukaje asibiti aka dubata kafin su dauki hanyar gida, ita dashi babu mai magana, sai yaronsu dake wasa da gwalantu a kwance a bayan mota.

Sai wajan biyar da rabi suka isa gidan.

Da kanshi ya bude mata motar ta fito jikinta duk yayi tsami! kafafuwanta ma rawa suke da kyar take tafiya, ya bita da kallo kafin ya girgiza kai ya sunkuya ya dauko d'ansa yasa a kafada ya bi bayanta dashi.

Zaune a gefan gado ya sameta ta hada ta gumi hawaye na zuba saman fuskarta.

Ya dora mata yaron a jikinta dan kuka yake alamar yana bukatar nono.

Nonon ta fito dashi tasa masa a baki ya kama yana tsotsa.

Kusan a tare suka sauke ajiyar zuciya ita dashi.

Yace." Naga kin sanya damuwa a ranki har da ciwo hakan da kike zai janyo miki wata damuwar. domin ita wannan matar lokacinta ne yayi, nasan kuma kin san da cewa mutuwa dole ce, baki da laifi tunda ke taimako ki kayi, Allah kuma da zuciya yake hisabi.

Taja hanci tana girgiza kanta tace." Wallahi nayi dana sanin zuwa garin nan, domin da nasan abinda zai faru da ban daga hankalina ba, ashe tsautsayi ne yake kira na."

Yace." Babu wani tsautsayi ko kinje ko baki je ba lokacinta ne yayi zata mutu saboda haka ki cire wata fargaba daga ranki.

Shuru tayi ba tace komai ba,

Ganin haka yasa ya nufi toilet domin wanke jikinsa shi kansa da fargaba da damuwa ya wuni ga wata irin yunwa da take damunsa.

Washe garin ranar da ta dawo Aunty Zeey tazo, sosai taji dadin zuwanta, suka dinga hira, har ta gaza boye mata abinda ke damunta ta sheda mata, ita kanta aunty Zeey din sai da jikinta yayi sanyi kuma ta tausayawa Hamra'un.

Suna tsaka da hira Madam da Nabila sukayi sallama.

Cikin sakin fuska ta amsa ta mike domin girmamawa. gurun zama take nuna mata, ita kuwa aunty Zeey din kamar wacce aka aikowa da mutuwar iyayenta, muraran ta fito da bacin ranta da kishinta.

Madam wayayyar macace mai ilimi da sanin ya kamata, ta kalleta da fadin." Zainab kina nan kenan."?

Ta dauke kai da fadin." Aikuwa."

Murmushi tayi kafin ta juya tana amsa gaisuwar da Zinat ke mata, a mutunce suka gaisa Madam tayi mata gaisuwa daman abinda ya kawota gidan kenan.

Aunty baki a tabe ta kalli Nabila da fadin." Ke kuma kin isa kenan babu wanda yake da mutuncin samun gaisuwarki a cikinmu.

Tace." Haba dai Aunty Wallahi ina ta gaisheki ba kiji ba sai nace bari ku gama gaishe-gaishe sai mu gaisa a nutse.

K'aramin tsaki taja ta kawar da kanta.

Itama Nabilan taji takaicin abinda tayi mata amma sai ta daure ta sake gaisheta, ta amsa kamar bata so.

Ta juya ta gaishe da Zinat din tare dayi mata gaisuwa. ta amsa a sake da nunawa kulawa.

Ba su wani zauna ba suka suka tashi da niyyar tafiya,  har bakin kofa ta rakasu tana godiya.

Tana juyowa suka hada ido da Zeey sai harararta take,  taja tsaki mai karfi kafin tace." Wannan matar kike wa ladabi matsiyaciya sumu-sumu macijin sari ka noke.

Ta zauna kujerar dake fuskantarta tace." Aunty zeey  me yasa kike zagin Madam ne? wallahi ni duk laifinta da kike fadi ba tayi min komai ba.

Tace." Dama yaushe za tayi miki tunda baku hada miji ba, matsiyaciya ai gashinan tana zaune da god'amemiyar 'yarta taki auruwa, babu mashinshini."

Cike da mamaki tace." Aa  kamar an sa ranar auranta.

Tsaki taja da fadin." A bakin wa ki kaji babu wani mai so bakin jinine da ita.

Yar dariya tayi kafin tace." A bakin maigidana naji cewar dashi aka karbi kudin auranta an sanya shekara guda.

Aunty Zeey jikinta yayi sanyi ta zuba mata ido da mamaki a tare da ita.

Tace." Wallahi kuwa kin san abinda yayi Asp shi yayi mijina shiyasa na samu labari.

Tace." Aikin banza to meye abin rufa-rufa dan ya fito ya fada min wani abune mtwwws! ni na rasa me yake damun Asp  wallahi matar nan gabad'aya ta shanye shi sai abinda tace masa.....

*Kada ki karanta min littafi idan baki biya,  kada ki siya ki fita dashi, 'Yar uwa kada ki ganshi a group kiyi shearing domin hakkina ne, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne.....0542382124...Binta umar gtbank. idan kati zaki turo sai kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[5/21, 7:53 PM] Matar 'Dan Aljannah: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya

muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

_*(Uwace  ita a gurina kuma 'Yar uwa ce, ina jin ita din kamar 'yar uwa ta ta jini, ta damu da damuwata😭 ta kasance kullum mai min addua da fatan alkairi, na rasa a wane matsayi zan ajiyata a zuciyata,  tana kira na da Mamana, ni kuma ina kiranta da Daughter, dalilin rubutuna muka hadu, tsayin shekaru hudu muna tare abin farin cikin kuma  muna gari d'aya, Daughter ZAINAB KHABIR ISHAK koda nisan in da kike ya kai birnin sin sai nayi fatan Ubangiji Allah ya sadamu da juna, to ballanatana  muna cikin gari daya,  wannan zumuncin zai cigaba da wanzuwa da ikon ALLAH.  na jinjina miki  k'warai Allah ya saka da alkairi🙏🏻)*_

*129*
Cikin nazari take kallonta tana auna maganganunta, ba tun yau ba ta lura da cewar tana da masifar kishi irin wanda ba a so, to idan ba hakaba meye laifin Madam mace mai mutunci da sanin ya kamata, a ganinta idan haka duk kishiyoyi suke to babu shakka za'a samu maslaha a zamantakewa, amma Zeey ta tsawwala da yawa, tunda suke da Madam bata ta'ba zagin Zeey ko ta fadi wata mummunar kalma a kanta ba, amma ita a koda yaushe cikin zagin matar take.

Ajiyar zuciya ta sauke tace." Zeey ki sanyawa zuciyarki salama don Allah kiyi tsaftataccen kishi, ba wai ina goyan bayan Madam bane amma a ganina kamar bata da matsala da zakiyi hakuri to babu shakka zaku zauna lafiya."

Tsaki taja da fadin." Na lura dai tsakaninmu babu amana fuska biyu gareki Zinat idan ba haka ba mai zai sanya a gabana kina goyan bayan mutsiyaciyar matar nan da kowa ya san da cewa mutuniyar banza ce wacce babu abinda tasa a gaba sai bin bokaye da  zinace-zinace  duk domin biyan bukatarta." cikin masifa da kumfar baki take maganar.

Ita dai tsabar mamaki kasa cewa komai tayi, kawai ta dinga kallonta tana jimanta al'amarin.

Tana cigaba da zagin Madam din ta lalubi mayafinta ta yafa, ta mike da fadin." Ni nayi nan ai yau na fahimci inda kika nufa kuma."

Ta mike da fadin."  wallahi Zeey baki da fahimta itafa rayuwa gabadaya hakuri ake da ita, amma duk kin bi kin tayar da hankalinki sai zage-zage kike akan kishiya wacce bata damu dake ba, ta mayar dake shashasha wallahi kiyi gaggawar gyarawa."

Ta watsa mata kallo mai muni kafin taja wani dogon tsaki fuuuuu! ta kama hanyar fita tana surutai marasa ma'ana.

Baki a bud'e ta bita da kallo har ta fita daga falon, girgiza kai tayi tana mamakin al'amarin, tabbas an san kishi halak ne amma a ganinta irin nasu aunty Zeey din ya sa'bawa sharia domin kuwa zuciya za ta sanya su aikata abinda ba shikkenan ba.
Ita dai zata cigaba da hakurin zama da Hamra'u tunda dai Allah yasa yarinyar ta gane gaskiya to sai suyi hakurin zama da juna.

*BAYAN WATA UKU*

Zaman lafiya da daidaito yake wanzuwa a gidan tun bayan dawowar Hamra'u babu wata matsala data sake faruwa, kowacce na kokarin kyautatawa 'yar uwarta hakan yayi wa Uwale dadi, sai dai kuma shi daga b'angaran uban gayyar babu wanda ya san abinda yake cikin zuciyarsa sai Allah sai kuma shi, amma yana bala'in jin haushin had'e masa kai da sukayi, idan Zinatu tayi magana a gidan to ta zauna, duk yanda yaso ya ruguza alakarsu ya kasa, a yanzu Hamra'u tafi jin maganar Zinatu a kan tashi maganar, babban takaicinsa kenan, zai bada umarni ayi abu amma idan ya dawo gidan sai ya tarar ba'ayi ba.

Hamra'u cikinta wata bakwai ta gaza komai ta lanjare abinka da mara jiki, cikin har rinjayarta yake saboda girmansa, anyi scanning an tabbatar da cewa twins 'yan biyu ne duk mata, wannan dalilin yasa likita ya kafa mata dokoki, wannan bai dameta ba tunda akwai kyakykyawar fahimta a tsakaninsu, gabadaya ta tattara mijin ta barshi a gurin Zinatu......Hakan yayi masa dadi mutuka, amma bai nuna ba, sai ma ya fara wasu irin zantuka domin neman magana da tada zaune tsaye.

Cike da mamaki ta kalleshi bayan ya gama maganganunsa.

"Ta nan ka bullo kuma."?
Ta fada tana masa kallo na rashin fahimta.

Yace." Eh kwarai kuwa ai gaskiya ce, gabadaya kin tattara komai kina zalintar 'yar mutane duk abinda ki kace shi za'ayi idan kina tursasa Hamra'u to ni baki isa ba."!
Cike da karsashi da kwarin gwiwa yake maganar.

Ta danne bacin ranta dalili ba taso suyi hayaniya hakan babu amfani, amma ta lura kwana biyu neman masifa yake da ita.

"Kai yanzu dan Allah ba kaji kunyar fadin wannan maganar ba."?

Shuru yay mata yana duba wayarsa.

Ta girgiza kai cikin 'kunar zuciya tace." Ka tashi ka tafi dakin nata ai ba rike maka kafafu nayi ba, domin bani na gayyatoka ba."

"Ba za'a tashi ba." ya fada yana watsa mata harara!

Ta daga masa hannu da fadin." To tunda abun ya kasance haka kaje can ku yanke shawara da matarka, amma kada ka kara shigo min daki ranar girkinta."

"Kin riga kin lalata min ita yaushe zanyi magana taji ta saurara."

Ta dinga kallonsa da mamakin furucinsa ta rasa wane irin hali ne dashi kwana biyu ya d'ora mata karan tsana masifar yau daban ta gobe daban.

Tashi tayi ta fita daga dakin ta barshi, shi kad'ai ya gama duk wasu uzurinsa ya fito cikin milk din jallabiya, tana zaune a falo tare da Marakisiyya suna kallo yazo ya fita yana baza 'kamshin turare, bayanshi tabi da kallo tana ayyana wasu abubuwa a kanshi gabadaya ya sauya halaye sai tsiro musu da abubuwa yake marasa dadi.

Babu kunya a daran ya lallabo da bukatarsa, aikuwa ta furje tace." Tunda yana zarginta da zalinci to yaje can gurin matar tasa ya biya bukatarsa itama ta daina yarda tunda abun arziki yana zama sharri

Yayi-yayi da ita ta'ki, sai ya shiga kwantar da kai yana yi mata dadin baki tai masa banza ta cigaba da gyarawa yaronta shimfida.

Kallonta yake yana lumshe idonsa lokacin tana sanye da karamar riga iya gwiwa mai santsi duk ta kwanta a jikinta komai yana gani a idonshi, hallitarsa ta sanja wata irin jaraba ce take cinsa. ya dinga wani micincina ido yana shafa gemunsa.

Ta gama komai ta nemi guri ta kwanta duk yana kallonta.

Kallonsa tayi da fadin." Idan zaka fita ka kashe min fitila.

Zazzafar ajiyar zuciya ya sauke kafin yace ." Kina tunanin kinfi karfina ko."?

Da sauri tace." Me za kayi min to ko ka danne ni kayi ta karfi babu abunda zaka samu."

"Haka ki kace."?

Shareshi tayi, ta gyara kwanciyarta tare da rufe jikinta da bargo.

Ya tashi yaje ya kashe fitila ya dawo gaba gadi gadon ya nufa.

Da sauri ta tashi zaune tana kallonshi yana kokarin cire rigar jikinsa.

Kamar ya san abinda take shirin aikatawa yayi gaggawar rike hannunta rikon tsauri yayi mata ya fara gudanar da abinda yake ganin shine mafita a rayuwarsa.

To da yake sun riga sun zama daya ya gama gane lagonta duk turjiyar da take masa abu daya yayi mata ta bada kai bori ya hau, dan har sai da ta fishi ficewa daga hayyaci! ita dashi a wannan fagen ba'a cewa komai🤭

*****
To har yanzu dai Commissioner yana kwance a asibiti tare da kyakykywar kulawa daga manya likitoci hakan ba yana nufin komai ya wuce ba, Aa ana so ya warware ma'ana ya samu sauki a yanke masa hukuncin da ya dace da abinda ya aikata a matsayinsa na wanda yayi rantsuwa da Allah cewa ya dauki amanar kula da k'asa da kuma al'ummar dake cikinta, iyalinsa na cikin tsantsar tashin hankali duk da cewa basu rasa komai ba na rayuwa amma tabbas suna da tabbacin cewa hukuncin da za'a yanke masa mai tsauri ne, dalilin gagarimin laifin da ya aikata na cin amanar k'asa.

******
Haihuwar Hamra'u tazo da tangard'a, wannan dalilin yasa babu shiri aka shiga da ita dakin fid'a domin ceto ranta da abinda ke kwance a cikin nata.

Anyi cikin nasara an ciro tagwayen mata kyawawa farare tas masu kama da ita lafiyarsu lau, itama kuma alhamdulillhi, ta tashi da hankalinta an kuma kira sunanta ta amsa.
Wannan ya sanya hankalinsu duk ya kwanta ganin yanda Allah ya takaita wahala komai anyi cikin nasara da amincewar ubangiji.

Allah kenan kana taka yana tasa, a daran Hassanar ta mutu ta bar Husainar, likita ya tsananta binkice gurin gano dalilin mutuwar yarinyar bai ga komai ba dan Ubangiji bai so ya gani ba, kawai dai ya kar'bi abarsa ne bayan ta nuna kamanni.

Ban ta'ba ganin kukan Umaru ba sai a ranar ya dinga share hawaye yana kallon Usainar yaso Allah ya hada duka ya bar masa domin da haihuwar yaran Allah ya jarabceshi da masifar son su.

Hakanan sukayi hakuri suka barwa Allah ikonsa.

Kwananta goma sha hudu sati biyu kenan aka sallamesu suka koma gida lokacin ta warware sosai tana iya komai da kanta sai dai wasu abubuwan Zinat din ke mata ko kuma ta sanya daya

daga cikin hadimanta suyi mata.

Kwana arba'in da biyu da haihuwar jini ya 'balle mata, hankali a masifar tashe suka nufi asibiti aka fara bata taimakon gaggawa!

Sai da kwana ta biyar a kwance a asibiti sannan ta samu sassauci, likita ya kafa sharudai da dokoki kafin ya sallameta suka koma gida.

Ba batun bin ba'asi ya shigo dakinta ya rufe ta da masifa ta inda yake shiga ba ta nan yake fita ba, a ganinsa Ita take cutar yarinyar har hawan jini yake so ya kamata.

Wannan al'amarin yayi bala'in 'bata mata rai! da yake shad'ain yana kusa! abinda yake so kenan! sai ya kara rura wutar rikicin suka dinga masifa yana fada tana fada karshe dai 'bacin rai yasa yace ta fitar masa daga gida, ita kuma tayi rantsuwa ita din 'yar halak ce sai ta fitar masa daga gida kamar yanda ya bukata. amma kafin hakan dole ta in da aka hau ta nan ake sauka.
Wayar Asp ta kira domin sheda masa halin da ake ciki...
[5/21, 7:53 PM] Matar 'Dan Aljannah: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*131*
Cikin girma da dattako aka saukeshi, yanda ake karramashi da mutuntashi ya sanyayar masa da jiki, anya kuwa zancan zucci yake shida zuciyarsa.

Gama cin abincinsa ke da wuya magajin sarki ya shigo, cikin sakin fuska da wasa da dariya suka sake gaisawa kafin ya isar da sakon da yake tafe dashi cewa maimartaba na bukatar ganinshi.

Duk kwarin kansa da jarumtarsa sai da gabansa ya fadi jin cewa maimartaba na bukatar su tattauna, ko babu wannan dalilin haka kawai mutumin yake masa kwarjini!

Yayi kokarin danne fargabarsa ya mike tare da aro jarumta yabi bayan magajin sarkin dan amsa kiran da ake masa.

Yaji dadin ganin sarkin shi kadai, ya cire takalmansa a nutse ya shiga fadar da sallama a bakinsa.

Shima ya amsa fuskarsa a sake  hakan zai nuna maka cewar yana farin ciki da zuwan Umar din.

Ya zauna kusa dashi daga kasan kafafunsa irin zaman rakuma yayi kai a kasa yake mika gaisuwarsa.

Cike da annushuwa ya amsa yana tambayarsa hanya tare da iyali."

Ya amsa da "Kowa lafiya lou ranka ya dade duk suna gaisheku"

Yace."Muna amsawa da kyau Umaru naji dadin zuwanka ina fatan dai babu wata matsala dake faruwa tsakaninka da iyalinka, domin ni babban burina a duniya ace yara na suna zaune a dakin mazajensu da dadi babu dadi ayi hakuri da juna domin shi aure ibadah ne, kuma jin dadinsa kadan ne don haka ayi hakuri da juna ana kai zuciya nesa."

Yayi kwatakes da jin nasihar da sarkin yake masa,  wannan ya tabbatar masa da cewa yarinyar bata gidan,  dan haka da sauri yace." Insha Allahu zamu kiyaye za kuma muyi iyakacin bakin kokarinmu gurin kwatanta adalci sai dai dan adam tara yake bai cika goma ba, ranka ya dade ina neman afuwa dangane da abubuwa na rashin dadi da suka dinga faruwa a can baya sharrin shadain ne, yanzu alhamdulillhi muna zaman lafiya da juna babu wata matsala da ikon Allah.

Yace." Alhamdulillhi Umaru babu wani bawa da zai kasance a duniya ba tare da kuskure ba, saboda haka kada ka damu dangane abunda kake tafe dashi, na amince da kai dari bisa dari, shine dalilin da yasa na dauki 'yata na baka aure, saboda haka magana tuntuni ta wuce a gurina, Allah ya kiyaye gaba."

Cike da kwarin gwiwa ya amsa da "Ameen." yana jin sanyi a zuciyarsa yanzu ya kashe matsalar yana da tabbacin cewa ko zuwa tayi ta kawo k'ararsa mahaifin nata ba zai saurareta ba.

Ya wani risinar da kai cikin sigar girmamawa yake ta godiya da irin alkairin da akayi masa

Wannan abunda yake ya kara kankaro masa daraja da mutunci a idon sarkin.

Tun a mota ya kira wayar Asp yake sheda masa abinda ke faruwa.

Asp din yace." Ikon Allah ni kuma kaga yanzu muka gama waya da ita ta bani tabbacin cewa tana KANO din gidan Hassana 'yar uwarta.

Dogon tsaki yaja ya girgiza kansa dake bala'in sara masa yace." Kaga ni yanzu na wucr bichi na kusa isowa gida amma tilas na juya baya tunda ka tabbatar min da gaskiya.

Sam bai bashi tausayi ba, yace." Eh hakan shine maslaha amma ka fara sheda mata zuwanka ta waya bayan haka kuma ka tanadi kalaman da zasu tausasa mata zuciya."

Ya hadiye wani kuttun takaicin da ya tokare masa a wuya, wai shin da Asp yake wannan maganar shi yafishi sanin abinda zaiyi, gabadaya ma haushin Asp din ya kamashi ya kashe wayar ba tare da yayi masa sallama ba.

A kalar motar ya juya da tunanin abinda zai faru idan suka hadu
[5/14, 6:44 PM] Matar 'Dan Aljannah: Sai bayan isha'i ya shiga unguwar tarauni a cikin unguwar gidan Hassanan yake, gidan bai bace masa ba duk kuwa da cewa zuwanshi daya.

Parking dinsa keda wuya mijin Hassanar ya fito daga gidan da cazbaha a hannunsa da alama massalaci zai shiga.

Ya karasa bakin motar yana mamakin maganinsa.

Akwai sabo a tsakaninsu duk da ba'a gari daya suke ba amma sa'i da lokaci suna gaisawa a waya.

Ya mika masa hannu suka gaisa cikin girmama juna.

Alhaji Sa'ido yace." Allah dai yasa lafiya Umaru na ganka cikin dare wallahi ba kaji yanda jikina yay sanyi ba.

Jin abinda yace ya sanya shima jikinsa mutuwar yace." Alhaji Zinatu ba ta gidanka kenan."?

Ya gyada kansa da fadin." Eh ai ni rabon da in sanya Zinatu a idona har na manta sai dai wani sa'in muna gaisawa a waya a duk lokacin da suke waya da 'yar uwata na kan bukaci ta bani ita mu gaisa."

Wani zazzafan gumi ya karyo masa, gabadaya ya rasa yawu a bakinsa kafafunsa ne ma suke rawa gabadaya ya rasa yanda zai bullowa al'amarin, kawai sai ya shiga kici-kicin bude mota ya shiga.

Alhaji Sa'ido yace." Umaru akwai matsalar da take faruwa tsakaninka da iyalinka ka nutsu ka

tsaya mu tattauna sha'anin mata sai hakuri."

Ya shiga motar ya zauna yana kokarin tayar da ita yace." Alhaji afuwa kayi min hakuri tabbas hasashenka gaskiya ne sai dai a halin yanzu bani da nutsuwar da zan tsaya nayi wata doguwar magana saboda wani dalili don Allah idan ka shiga gidan ka mika min gaisuwata."

Jiki a sanyaye yace." To shikkenan Allah yayi mana magani, Allah ya kiyaye hanya."

Ya amsa da "Ameen ya rabbi Alhaji na gode kwarai."

Alhaji Sa'ido bai gusa da gurin ba har sai da ya ga b'acewar motar daga layin gidan nasa sannan yayi addua a zuciyarsa ya kama hanyar massalaci kamar yanda ya dauki niyya.

Sai da ya hau titi sosai sannan ya lalubi wayarsa dan ya gaza hakuri yana tokin motar ya kira wayarta.

Ta daga da sallama , a bakinta.

Muryarsa ya raunata da fadin." Kina so zuciyata ta bindiga ko."?

Tai masa shuru ba tace komai ba.

"Kin mayar dani shakatafi kina min yawo da hankali so kike na kwana a kan kwalta ina galantoyin neman in da kike."

Zumbura baki tai da fadin." Na maka fa ina gidan Aunty Hassanata"

Ya fesar da wani zazzafar huci! cikin kunar zuciya yace." Daga can nake kuma Alhaji Sa'idu ya tabbatar min da cewa bakya nan okey tunda kina so na shiga tsakiyar motoci su bugeni shikkenan bukatarki sai ta biya." Da sauri ya kara karfin motar ya figeta da mugun gudu!  yana sane yayi hakan.

Aikuwa hankalinta ya tashi jin k'ugin motoci da iska a kunnanta.

Kashe wayarsa yayi ya Ajiye ya saisaita tafiyar da motar.

Gaza hakuri tayi ta fito daga daki hankalinta duk a tashe take shedawa Asp abinda yake shirin faruwa.

Yace." Rabu dashi duk barazana ce kada ki kuskura ki sheda masa kina gidana."

Maganar sam bata gamsheta ba,  gabadaya ma hankalinta ya karkata kansa.

Ta dauki waya ta kira shi  sai da ta kusa katsewa ya daga, bai saurari maganarta ba yace." Sha biyu dai-dai na dare za'a kawo muku gawata."

Gabanta yana faduwa tace." Wace irin magana ce wannan ka daina don Allah."

Yace." Allah idan baki fada min inda kike ba to ba zan dawo gidan da lafiya ba, gani ma zaune a mota cikin wani daji."

A sanyaye tace." Amma dai kasan abinda kayi baka kyauta ba ko."

"Na sani kuma na baki hakuri ai kowane dan adam yana laifi mai zai sanya ba zaki yafe min ba."

Sanyayyar ajiyar zuciya ta sauke a hankali tace." Na yafe maka  amma don Allah kada ka kara zargina da wani abu bana jin dadin hakan Hamra'u da 'ya'yanta bani da nufin cutar dasu.

Ya sake jin wani sabon so da kaunarta na ruruwa a zuciyarsa......."Zinatu baki da matsala dani na amince dake dari bisa dari na kuma tabbatar da cewa ke alkairi ce a tare dani abinda ya faru tsakaninmu sharrin shadain ne amma da izinin Allah hakan ba zai sake faruwa ba.

Ta sauke ajiyar zuciya da fadin." Ameen ya Allah yanzu kana ina."?

Ya gyara zamansa kan kujerar motar da fadin." Ina hanya insha Allah nan da lokaci kankani zan iso ina fatan nazo na sameki a gidana."

Tace." Insha Allahu dama banyi nisa ba, ina gidan abokinka."

Cike da mamaki yace." Wa kenan."?

Jim tayi kafin tace." Wa kake dashi bayan Asp ina gidanshi."

Murmushin takaici yayi yace." Dama sai da na zargi hakan a zuciya wato hada baki kukayi domin ku wahalshe ni ko ."?

Murmushi  tayi ba ta iya cewa komai ba.

Yace." Zan kashe waya amma ki tabbatar da cewa na sameki a gida."

Tace." Kada ka damu kai dai kayi draving a nutse."

Yace." Insha Allah."

Kashe wayar tayi tare da tunanin yanda za'ayi ta iya fita daga gidan,  tana jin kunyar Asp sosai amma dole tabi umarnin mijinta tunda ya gane kuransa yanzu ta tabbatar da cewar tana da muhimmanci a rayuwarsa.

Allah ya taimaka Asp din a gidan Zeey yake, taji dadin hakan sosai, amma kuma boy yaronta yana gurin Nabila dan tunda suka zo gidan take dawainiya dashi nono ne kawai yake kawoshi gurinta.

Wata shawara ta yanke a zuciyarta, hijab dinta tasa ta fito falon  babu kowa duk suna daki da sauri ta kama hanyar fita shawarar data yanke kenan daga baya an kawo mata yaron.

Kai tsaye Side dinsu ta nufa,  da yake bracck din akwai haske bata samu matsala ba, sai dai haushin karnuka da suka cika mata kunne.........Kai tsaye sashenta ta nufa zuciyarta cike da tunane-tunane masu kyau da marasa kyau.

*Kada ki karanta min littafi idan baki biya,  kada ki siya ki fita dashi, 'Yar uwa kada ki ganshi a group kiyi shearing domin hakkina ne, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne.....0542382124...Binta umar gtbank. idan kati zaki turo sai kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[5/21, 7:53 PM] Matar 'Dan Aljannah: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

Asp yasha mamaki lokacin da Madam ke sheda masa cewa Zinat bata gidan,  koda ya kira wayarta domin ta bashi tabbacin inda take, sai ta hau inda-inda,  da yake mutumin yana kusa da ita shi ya k'arbi wayar yayi gyaran murya Asp yaji muryarsa ta doki kunnunsa, shuru yayi yana  mamakin al'amarin.
Yace." Gata nan a kusa dani wahala ta ta k'are ai na fad'a maka dama ba'a shiga tsakanin masoya."

Maganar ta bashi dariya yayi kadan kafin yace." Dama ni na isa na shiga tsakaninku? kawai dai nayi hakan ne domin na nuna maka kuskuranka amma banyi  da wata manufa."

Ya sauke ajiyar zuciya da fadin." To daka kai har ita abinda ku kayi min sai Allah ya saka min."

Cike da mamaki yace." Yanzu dai  Kana so  mu nemi gafararka kenan?

Yace." Kwarai kuwa shine samun nutsuwarku domin Allah ne kadai yasa da sauran kwana na a gaba da tuni sai dai labari na."

Asp ya fashe da dariya da fadin." Ai na kara tabbatar da cewar duk wata burga da kake da fuffuka  k'arya ce wannan yarinya itace rayuwarka gabadaya kwana biyu kacal duk ka susuce kamar ba jarumin namiji ba."

Ya shafa gemunsa yana mata wani sihirtaccan kallo  hannunta ya sake rintsiwa a cikin nasa yace." Asp sanin abinda ke zuciyar mutum sai Allah sai kuma shi wanda zuciyar take jikinsa amma kana hasaso gaskiyar abinda ke cikin zuciyata wannan shine gaskiyar magana."

Ajiyar zuciya ya sauke da fadin." Alhamdulillhi abokina nayi farin cikin hakan, kuma ina rokon Allah yasa wannan abunda ya faru a tsakaninku ya zama karshen matsalarku, Allah ya kore fitina a tsakaninku."

Cikin farin ciki da jin dadi ya amsa da "Ameen suma ameen mutumin kirki na gode kwarai da kokarinka a kaina da kuma iyalina,  ina rokon Allah ya bani ikon kyautata maka."

Ya amsa da ameen ya rabbi kafin suyi sallama cikin karamci da mutunta juna.

*****
To alhamdulillhi bayan faruwar wannan matsala wani abu mara kyau ko tashin hankali bai sake faruwa ba a tsakaninsu, duk wasu tunane-tunane da yake marasa kyau a da ya ajiye ya daina, yana kokarin kyautatawa iyalinsa shi kansa sai yanzu ya gane cewa zaman lafiyar da suke shine kwanciyar hankalinsa.

****
Kowa ya san dai abinda commissioner ya aikata ya sa'bawa dokar 'kasa wannan dalilin yasa bayan ya warware aka gurfanan dashi a gaban mai sharia, ba tare da jayayya ba ya amsa laifinsa, wannan dalilin yasa mai sharia ya sasauta masa, amma tabbas hukuncin kisa ne a sauka a kanshi, saukakawa sharia da yayi baiyi jayayya ba yasa mai sharia ya yanke hukuncin cewa a kai shi can gidan kaso (prison) na tsayin shekaru biyar kafin a kashe shi.
To ya za'ayi, bahaushe yace." Son zuciya 'bacin ta, zuciya mugun nama idan kabi ra'ayinta ta kai ka ta baro, Allah kasa mufi karfin zuciyoyinmu.

A ranar da aka tasa 'keyar Commissioner of Police gidan kaso (prison) a ranar aka mayar da Asp kujerarsa wato shugaban 'yan sanda abokinsa Umaru GOJE ya maye tashi kujerar mai taken kakakin rundunar 'yan sandar jahar KATSINA. haka abokan suka wanzu cikin hidimtawa al'umma da kare 'kasa tare da abinda ke cikinta.

****
"Aunty Maijidda miliyan biyar nakeso ki bani aro."

Kai tsaye ya fadi maganar idonsa 'kuri a kanta.

Ta kalleshi ta sake kallo takaicinsa duk ya cika mata zuciya tace." Sadiq ashe baka hankali don ubanka me za kayi da miliyan biyar."?

Ya 'bata rai da fadin ." Kinga aunty Maijidda babu ruwanki da abinda zanyi da ita kawai ki bani bana bukatar surutu."

Tace." Bani dashi ka tashi kuma ka fice min daga gida mara mutumci"

Cikin fusata ya buga hannun kujera ya mike tsaye yana huci! da numfarfashi yace." Ni kike kira mara hankali "?

Tace." Eh kai ne mara hankali Sadiq ko zaka dake ni ne."?

Ya zabura! kamar zai kai mata mari! tayi saurin gocewa gabanta na faduwa take kallonsa.

Ya cize baki yana hura hanci da fadin " Zaki gane baki da wayo sai na tona miki asiri."

A gaggauce ya kama hanyar fita.

Da karfi ta kira sunansa "Sadiq." ko juyowa bai yi ba ya bude kofa ya fita kai tsaye fadar sarki ya nufa da yake safiya ce fadar sarkin cike take da jama'a 'yan uwa da abokanan arziki da kuma masu zuwa sulhu da sasanci.

Cikin rashin kintsi ya shiga fadar,

gabadaya ido yayi caa! a kansa.

Guri ya samu ya zauna ya tsirawa sarkin ido tamkar wanda yake binsa bashi.

Sarkin jikinsa yayi sanyi haka kawai yake tausayawa yaron, rayuwarsa ta gurbata gurin shaye-shaye da rashin kintsi da kamun kai. wannan dalilin yasa duk abinda yaron ya bukata daga gurinsa yake tallafa masa.

Gyaran murya yayi a nutse ya kira sunansa.

Ya amsa yana me sunkuyar da kansa kasa

Yace." Kana bukatar wani abu daga gurina.

Yayi shuru yana dawurwura! har yanzu idon jama'ar dake gurin na kansa.

Sarkin ya kalli shamaki dake kusa dashi yace." Wannan yaron ga dukkan alamu akwai abinda ke tafe dashi a kawo min shi kusa dani domin naji daga gareshi."

Shamaki ya kamo hannunsa ya tsuganar dashi gaban Sarkin kafin yace." Yaro kada kaji tsoro ka fadi abinda ke tafe da kai,  ni ina magana ne da yawun sarkin dake gabanka a halin yanzu.

Sadiq wani irin gumi ya fara yanko masa.

Wai shin ma ya akayi ya kawo kanshi gurin nan?

Idan ya tonawa 'yar uwarsa asiri ai tare suka had'u suka shirya sharrin tilas shima ya fuskanci hukunci .

Cikinsa ya duri ruwa ya dinga wani irin k'ugi  kai Allah ya tsinewa (kamru uwar laifi) sai yanzu ta sake shi ya gane wautar da yake kokarin tafkawa.

Alamun rashin gaskiya ya bayyana a tare dashi sai gumi yake sharcewa ya kasa cewa uffan sai magana ake masa.

Sarki a jikinsa yake ji akwai matsala dan rashin gaskiyar dake tare da yaron yafi komai daga masa hankali, addua yake akan Allah yasa ba zuwa yayi ya kashe rai ba.

Ba zato ba tsammani!  Sadiq yaji saukar tsabga a bayansa.

Ya gantsare tare da kurma uban ihu!  idonsa akan dogarin dake tsaye a kansa da murtukekiyar bulala a hannunsa sai zare masa ido yake.

Cikin hargagi!  yace." Hattara 'yan samari nan ba gurin harigido bane ba gurin gardama da jayayya bane yi kokari ka fadi abinda ya kawo ka Sarki yana sauraranka."

Bulalar ya daga da niyyar sake zabga masa Sarkin ya dakatar dashi.

Ya sauke hannunsa da fadin." Gyara kintsi! Allah ya 'karawa sarki lafiya."

Fadar tayi shuru na 'yan mintina, kafin a nutse Sarki ya kalleshi da fadin." Abubakar Sadiq ni abinda nake hasashe shine  kaje ka dauko magana a cikin gari kazo ka gurfana a gabana domin na zame maka garkuwa to ka sani cewa ni UMARU ba zan lamunci zalinci ba duk irin hukuncin da ya cancanta da abunda ka aikata shi za'a yanke maka."

Ai kawai sai ya fashe da kuka! ya rike kafafunsa da fadin." Ranka ya dade ka gafarce ni wallahi ba laifi na bane duk abunda ya faru Aunty Maijidda ce ta bamu umarni."

Jin ya ambaci sunan amaryarsa yasa ya tsira masa ido da mamaki a tare dashi.

Daga farko har karshe ya warware yanda akayi suka shirya sharrin amma beyi tasiri ba, tunda wacce sukayi niyyar sabautawa rayuwa  addua iyaye na tasiri a kanta, tana dakin mijinta a halin yanzu har da zuria  a tsakani.

*Kada ki karanta min littafi idan baki biya,  kada ki siya ki fita dashi, 'Yar uwa kada ki ganshi a group kiyi shearing domin hakkina ne, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne.....0542382124...Binta umar gtbank. idan kati zaki turo sai kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[5/21, 7:53 PM] Matar 'Dan Aljannah: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai

domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

_*Mafi akasari masu bibiyar littatafan BINTA mutane ne masu mutunci da karamci da kuma dogon tsinkaye! babu yanda za'ayi suci zarafi na ko su gaya min mara dadi koda kuwa kuskure nayi cikin hikima zasu tunasar dani domin na gyara, amma abin mamaki wasu cima zaune da ban san da zamansu ba, sune suke cin zarafi na bayan sun karanta littafina har suna kirana da wasu kalmomin da basu cancanta ba, NAGODE bahaushe yace anayi da kai gwara ba'ayi da kai matakin NASARA ne, da yawa masu tsinkaye sun fahimci inda na nufa a cikin wannan littafin nawa mai suna GOJE! Alhamdulillhi naji dadi masoya da kuka bani goyon baya har Allah yasa na kammala isar da sakon dana dauko. Kunyi da aljihunku kana kuma kunyi da muryoyinku, Littafin GOJE! yazo da sabon salo kowa ya sheda hakan, ina rokon Allah ya bani rai da lafiyar da zan cigaba da nishad'antar daku tare da wa'azantarwa. daga karshe nake baku hakuri sakamakon tsaikon da littafin ya dinga samu bayan ya dauko gangara! kuyi hakuri insha Allah hakan ba zata sake faruwa ba🙏🏻*_

*GOJE*
*(SADAUKI OMAR RETURN*)

*END🔚*
*ALHAMDULILLHI*
*134*
Ya kalleshi cikin jadadda aniyarsa yace." Da gaske nake magana ba wai da wasa ba inaso ka bani auran yarinyar nan domin hakan shine maslaha a gare mu bakidaya." Shuru yayi na minti biyu kafin ya cigaba da cewa.'' Kasancewar mun riga mun sanar da jama'a ranar daurin aure a yanzu abune mai wahala gami da jin nauyi mu sake sanarwa mutane cewa lamarin auran ya lalace duk da cewar ba daga bangaranmu aka samu matsala ba amma da kunya, wannan dalilin yasa naji sha'awar auran yarinyar a cikin raina nasan daga 'bangaran ka ba zan samu

matsala ba sai dai daga ita yarinyar idan da hali ka sheda mata al'amarin idan ta amince Alhamdulillhi."

Ajiyar zuciya ya sauke kafin yace." Ban yi mamakin faruwar wannan al'amarin ba Umaru, nasan komai yana tafiya ne cikin kudirar ubangiji, wani baya auran matar wani haka zalika wani baya haihuwar dan wani, tabbas daga 'bangarena baka da matsala, zanfi kowa farin cikin kasancewar hakan, sai dai akwai gagarimar matsalar da nake hangowa mutukar al'amarin nan ya tabbata."

Murmushi yayi a nutse yace." Ka kyautata zaton alkairi abokina wannan al'amari da zai faru insha Allah alkairi ne, matsalar dai bai wuce ace rashin amincewa daga 'bangaran iyalina ba, kada ka damu da wannan, a yanzu akwai kyakykyawar fahimta a tsakaninmu, insha Allah zan zaunar dasu na fahimtar dasu yanda al'amarin ya kasance, burina shine ita yarinyar ta amince shikkenan sai komai yazo cikin sauki."

Yace." Hakane Allah ya tabbatar da alkairi maganar Nabila kuma zan zauna da ita a yau da ikon Allah komai zai zo da sauki za kuma mu tattauna da mahaifiyarta."

Cikin farin ciki ya mika masa hannu sukayi musabaha da juna kafin yayi masa sallama ya kama hanyar fita. Asp din ya bishi da kallon mamaki! hakane kowane mutum da akwai ranarsa, dama fargabarsa jin kunyar jama'ar daya gayyata ace kamarshi commissioner 'yan sanda ya gaza gano wanda yazo gidansa da niyyar auran 'yarsa, wannan shine babban takaicinsa, amma cikin ikon Allah abokinsa ya rufa masa asiri a lokacin da yake cikin tararrabi, tabbas zuciyarsa tayi na'am da abokin nasa, baya fargabar bashi auran 'yarsa, domin shi yafi kowa sanin halinsa.

Tana cikin k'unci da damuwa sakamakon yaudarar da Sulaiman yayi mata, sai gashi Ubangiji yayi mata tagomashi da samun nagartaccan namiji, koda mahaifin nata ya sheda mata niyyar abokinsa a kanta, babu jayayya ta amince, domin dama can tun fil-azal mutumin yana burgeta da kyawawan dabi'unsa, gashi d'an gayu kyakykyawa kuma jajurtaccan namiji, babu ruwanta da matansa, tunda shi ya bukaci auranta ta amince Allah ya sanya alkairi, to itama Madam tayi farin cikin faruwar hakan, domin dama tana cikin halin damuwa da takaici sai gashi Allah ya share musu hawaye ya maye musu gurbi da namijin da yake da wahalar samu a wannan zamanin, tayi addua sosai tare da fatan zaman lafiya madawwamiya.

To da yake a gidan Zeey yake bayan sun gama tattauna maganar sai yayi musu sallama ya tafi, koda yaje can din ma kasa shuru yayi dole itama tana da hakki ta san abunda yake faruwa a matsayinta na matarsa, nan ya sheda mata duk abunda yake faruwa.

Ko a jikinta dan bata nuna wata damuwa ba ko farin ciki ba, sai dai a can kasan zuciyarta taji dadin kasancewar hakan, yanzu ai dole ita Zinat din ta san wacece Madam da makircinta.

Washe gari Asp din yana fita ta dauki waya domin kiran Zinat din.

Lokacin suna tare da maigidan yana shirin fita gurin aiki.

Ta daga wayar suka gaisa kamar gaske, can kuma sai Aunty Zeey din ta fashe da wata mahaukaciyar dariya kamar sabuwar kamu.

Shi kansa Umar din dake can gefe a zaune sai da yaji taratsin dariyar.

Tace." Aunty Zeey me yake faruwa ne nifa matsala ta dake kenan."

Ta tsagaita dariyar da fadin." Murna na kira nayi miki"

Tace." Wace irin murna kuma."?

"Au zaki nake ni kenan." cikin zaurance tayi maganar.

Tace." Bangane hausarki ba don Allah kiyi magana ta fahimta mu gama na sallami mijina zai fita gurin aiki."

Cike da mamaki tace." Sannu da kokari gaskiya na jinjina bajintarki amma ina zargin munafikin mijin naki bai sheda miki cin amanar da suka kulla miki ba."

Gabanta ya yanke fadi, da sauri ta kalli gefan da yake, yayi saurin dauke kansa yana sake tamke fuskarsa, cigaba yayi da daura blet dinshi.

A sanyaye tace." Don Allah kiyi min bayani.

Tace." Oh!oh! wa'ka a bakin mai ita tafi dadi nasan dai komai nisan jifa kasa zai fado amma dai ki zauna cikin shiri nan da kwana uku zakiji bud'a! "Ayyiririririri!!!!." kawai sai ta kashe wayar tana kyalkyala dariya.

Kafafunta sukayi sanyi kalau da kyar take jansu ga ciki tirtsitsi a gaba ta iske inda yake tsaye da turare a hannunsa.

Wani irin  yanayi ya shiga ganinta cikin muguwar damuwa! ya riga yaji komai  matar abokinsa ta fasa k'wan wanda dama yana shirin fasa shi a ranar.

Hannuwansa ya bude tana zuwa ya rungumeta yana shafa gadon bayanta cikin nutsuwa yasa bakinsa a kunnanta ya sanyayyar da murya a hankali yace." Ta fada miki zanyi aure ko."?

Kanta ta dago tana kallonshi kafin tace." Tayi min jirwaye dai! nasan dama akwai wannan ranar tunda kasha fada min cewa kana da burin auran mata hudu to amma me yasa ka boye mana ai wannan munafurci ne."

Yaji haushin kiranshi da tayi munafiki, amma sai ya danne yace." Ki dinga tausasa harshenki gurin yi min magana ban ji dadin wannan kalmar da kika kira ni da ita ba."

Tayi saurin cire jikinta daga nashi, tana masa wani irin kallo kafin tace." To wane suna ka dace dashi? shin idan ka sheda mana cewa za kayi aure zamu hana kane."?

Ya daga mata hannu da fadin." Ya isa kada ki zage ni."!

Ya zuba masa rikitattun idanuwanta dake cike da fitina!

Ya duba agogon dake daure a hannunsa, lokaci ya kure babu damar ya tsaya yi mata dogon bayani, kawai ya kama hanyar fita ba tare da yace mata komai ba.

Da sauri ta tare masa hanya duk ta firgice kamar yau ne ranar da aka farayi mata kishiya.

"Wacece wacce zaka aura."?

Wannan tambayar tayi masa.

Sai kawai yaga babu amfanin jayayya a tsakaninsu, tunda ta bukaci sanin ko wacece bari kawai ya sheda mata ya wuce gurin.

" Kayi shuru kana kallona ga alama baka da gaskiya."
Ta sake narka masa wata bakar maganar.

'Bacin ransa ya danne kafin ya daidaita kansa yace." Nabila ce."

Wani irin murda cikinta yayi jin sunan wacce ya kira, a take gabadaya jikinta ya kama rawa!!

"Nabil.....Nabila wacece haka."?

Ta tambayeshi idonta a tsaye a kansa.

Kauda kansa yayi kafin yace."  Yarinyar abokina Asp nasan yanzu kin gan......Kafin ya karasa maganar ta daddage ta kurma ihu! tana rike kanta!

"Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!  ya kira kafin yay gaggawar rike ta yasa a jikinsa, cikin dakin suka koma tana ta tuttureshi yana sake riketa, wasu mugwayen hawaye ne suke ambaliya a fuskarta.

Yaji zuciyarsa tana nema ta karye  koda yayi yunkuri tashi ya tafi aiki  sai ya kasa, bayaso ya fita ya barta cikin wani hali.

Ta dinga kuka tana kallonshi! bakinta sai rawa yake tsabar tashin hankali da mamaki ya hana ta magana.

Shima nasa idon yana kanta gabadaya jikinsa yayi sanyi ya rasa da kalmomin da zai rarrasheta.

Sai kawai ya cire kakin jikinsa ya nemi guri ya kwanta baya tsammanin zuwa gurin aiki a cikin wannan yanayi.

Murya a dashe tace." Dama can kai kake neman auranta shine saboda munafurci ka boye min har  da cewa da kai aka kar'bi kudin auranta."

Ya tashi zaune yana kokarin tarairaiyota jikinsa ta janye ta matsa can gefe har yanzu kukan take tana masa wani irin kallo na ba kayi min adalci ba.

Murya a raunane yace." Bani bane daga baya Allah ya juya al'amarin kaina Zinatu ki nutsu nayi miki bayani abinda ya faru."

Hanci taja ba tace komai ba kawai ta zuba masa ido tana sauraransa.

Ya sake raunana murya tunda ya gane hakan da yake yana saurin kassarata shiyasa ya mayar da hankali.........Cikakkenan bayani yayi mata yanda zata fahimta sosai ya kuma shigo da maganar bazawarsa wacce da yake neman auranta a boye ya dora da fadin." Dalilin faruwar wannan al'amari na janye auranta ba don bana sonta ba, sai dai domin na rufawa abokina asiri, kuma ni a ganina auran Nabila ba matsala bane a tattare damu bakid'aya! a matsayinki na uwargida nake neman alfarma a gurinki cewa ki kwantar da hankalinki kada kiyiwa al'amarin mummun zato!  kisa a ranki cewa babu yanda Allah baya juya alamarinsa! inaso kuma ki sani

cewa har yanzu matsayinki na nan a cikin zuciyata, babu wata mace da zan aura da zata fiki matsayi a gurina, samun zaman lafiyar gidana yana tattare dake, gabadaya kece zaki wanzar da samuwarsa  idan kinyi min haka kin gama min komai wallahi.

Gabadaya jikinta ne ya mutu, maganganunsa sun kassarata mata jiki! ya fita gaskiya! ta ko'ina, kuma bata da wata hujjar da zata ha nashi auran yarinyar,  idan ta cika 'yar halak to yana da kyau ta marawa mijinta baya, ma'ana ta bashi goyon bayan auran Nabila dalilin mutunci da karamci da dattakon Asp yafi karfin komai a gurinsu, wannan dalilin yasa zuciyarta tayi sanyi ta amince da auran, babban farin cikinta, yarinyar tana da tarbiya kuma tana ganin mutuncinta, amma dole ta sake jadadda masa cewa ya ja mata kunne tun kafin ta shigo gidansu a tsare yake basa bukatar wani tsari nata kawai tazo bi shine kwanciyar hankalinta.

Da yake neman kwanciyar hankali yake a gidan nasa yace." Insha Allah ta kwantar da hankalinta babu wata matsala da zasu samu da yarinyar, amma dai duk da haka zai sake jadadda mata cewa dole ta basu girmansu.

Sai daf da sha biyu ya tafi gurin aiki. Asp ya sameshi a ofis yana duba wasu takardu suka gaisa a tsanake kafin ya sheda masa cewa Yarinya fa ta amince sai dai fatan zaman lafiya da juna. Yayi farin cikin jin haka daga gareshi godiya ya shiga yi masa bakinsa kamar gonar audiga, shi kuwa Asp din da yake akwai barkwanci sai ya shiga tsokanarsa yana kiransa da ANGO!  sai washe baki yake suna tsokanar junansu kamar ba surukan juna ba.

****

A daran itama Hamra'u  ya sheda mata abinda ke da akwai, aikuwa basu rintsa ba, dan kwana tayi tana kuka da rokonsa ya janye auran! kada ya kawo musu wacce zata lalata musu zamantakewa.

Duk yanda yaso ya fahimtar da ita abun yaci tura sai kawai ya rabu da ita ya shirya ya fita gurin aiki.........Da kyar Uwale da Zinat suka fahimtar da ita, sai daga baya itama ta gane cewa Asp ya wuce haka a gurinsu.

A cikin kwanaki biyun da suka rage soyayya ce mai karfi ta kullu a tsakaninsu, A waya yake kasheta da kalamai tun tana jin kunya da nauyi har ta sake itama ta fara mayar masa da martani. gabadaya idonsa ya rufe ya manta shaf da cewa ita din fa yarinyar abokinsa ce, koda yake ai NAMIJI ba abun kunya ne a gurinsa.

A na gobe daurin aure yaje har gidan Asp din da sunan zance a cewarsa yana so su tattauna da amaryarsa.

Asp kunya ta kamashi kawai sai ya girgiza kai domin al'amarin abokin nasa a yanzu mamaki yake bashi.

Dabararsa ta zuwa shine ya jadadda mata manufarsa cikin wayo da dubara yake nuna mata zamantakewar gidanshi cewa tayi hakuri da matanshi ta kuma dauke kai akan duk abunda zai faru, duk abunda ta tarar a gidan tabi mutukar bai sa'bawa sharia ba, insha Allah shi kuma yayi alkawarin kwatanta adalci a tsakaninsu.

Taji dadin bayaninsa domin munafikin namiji sam beyi ba a rayuwa, da alama shi wannan daban yake a cikin maza.

Nan ta tabbatar masa da cewa insha Allah tayi alkawari daga 'bagaranta wata matsala ba zata faru ba.......!

*Wannan  shine karshen labarin GOJE! ina rokon Allah ya yafe min kuskurena.....Allah kuma yasa a amfana da abunda na rubuta! Allah yasa damu da alkairi masoya NAGODE sai mun sake haduwa daku cikin wani littafin nawa mai zuwa da yardar ALLAH*

*Kada ki karanta min littafi idan baki biya,  kada ki siya ki fita dashi, 'Yar uwa kada ki ganshi a group kiyi shearing domin hakkina ne, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne.....0542382124...Binta umar gtbank. idan kati zaki turo sai kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[5/21, 7:53 PM] Matar 'Dan Aljannah: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita

kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*133*
Shuru fadar ta d'auka bayan k'are jawabin da ya hargitsa tunanin duk wanda yake zaune a gurin.
Bahaushe yayi gaskiya da yake fadin da d'an gari akan ci gari, ashe dama da sanya hannun Maijidda gurin faruwar al'amarin da ya tashi hankalin masarauta da duk wanda ke cikinta, tunaninsa bai taba kawo masa cewa Maijidda za taci amanarsa ba, ashe duk abunda take akan iyalinsa na ganin idone dama Aysha ta jima tana jadadda masa cewa ba mutuniyar arziki bace amma baya yarda da maganarta, cikin ikon Allah sai gashi yau ya tabbatar da maganarta.

Ya kalli Sadiq dake gurfane a gabansa yana zabga wani irin gumi! ya zubar da hawayen har ya gaji fargaba da tashin hankali duk sun dabaibaiye shi.

Ga mamakin duk wanda ke zaune a gurin sai kawai sukaji yace ." Ka tashi kaje Allah ya shiryeka tare da masu irin halinka."

Galadima ya kalleshi da fadin." Allah ya baka nasara iyakar hukuncin kenan."?

Murmushin takaici yayi kafin yace." Galadima wannan shine hukuncin da nake ganin zan iya dauka akan zuriar Malam Buba, sun ci albarkacinsa abinda suka niyyata ya faru Allah ya takaita, ita yarinyar yanzu haka tana dakinta zaune kalau wannan shine babbar nasarar da muka samu."

Gabadaya fadar ta cika da kabbara "Allahu akbar"! an gaishe da adalin sarkin mai aiki da ilimi da sanin ya kamata, adalin sarki ne wanda za kayi masa laifi shi ya saka maka da alkairi UMARUL-FARUK kenan, haka duk masu irin sunan suke akwai tausayi da kyauta kulawa da sadaukarwa hakuri juriya cikin ko wane hali.

Gabjejan dogarin dake tsaye a bakin kofa ya bugawa Sadiq din tsawa tare da nuna masa hanyar fita." Ganin yanda jikin dogarin ke rawa yasa ya tsorata da sauri ya mike takalmi a hannu ya kama hanyar fita daga masarautar yana godewa Allah da ya takaita masa wahala.

Ya jima yana tunanin ta yanda zai tunkari Gimbiyar tashi da maganar saboda sanin halinta amma ya zama dole ya sanar da ita domin tana da hakki akan hakan.

Ya gama yi mata bayanin komai tana sauraransa amma ba taji irin hukuncin da ya yankewa Maijidan ba.

Tace." Yanzu ita Maijiddar wane hukunci ka yanke a kanta kasan dai wannan abunda ta aikata dole a dauki mataki saboda gaba."

Shuru yayi yana nazari.

Tace." Nasan dama wannan matar ai ta gama da kai babu wani mataki da zaka dauka a kanta, shikkenan ni zan dauki mataki idan kai ba zaka dauka ba."

Ya kalleta da fadin." Wane irin mataki zaki dauka wannan maganar fa na fada miki ne saboda a fita hakkinki amma daukar mataki ba'a hannunki yake ba.

Ta fusata! da fadin." Idan ban dauki mataki akan Maijidda ba kace ni ba 'yar halak bace."!

Ya zuba mata ido yana kallo da bacin ran maganarta a tare dashi.

Safah ta shigo ta same su suna kallon juna sai kace zakaru! kowanne ransa a 'bace!

Guri ta nema ta zauna a nutse tace." Allah ya kori shaidan din da yake kokarin ratsa tsakaninku.

Ta kalleta da bacin rai a tattare da ita ta shiga sheda mata abunda ke faruwa.

Itama rai a bace tace." 'Yar uwa bake kadai zaki dauki mataki ba nima zan dauki mataki akan Maijidda domin wannan abunda ta aikata bai kamata a zuba mata ido ba."

Ganin sun hada kai yasa ya sassauta yana so su saurareshi.

Fafur! suka ki sauraransa ko wacce na kawo masa hujjojinta.

Yace." To yanzu ya kuke so nayi? Aysha ke kin san irin taimakon da Malam Buba mahaifinta yayi min ya kuma yi miki a lokacin da yake raye to mai zai sanya bayan ransa na wukalanta bayansa

Tace." Malam Buba daban Maijidda daban ai ganin hakan yasa take duk abinda takeso to wannan karon ba zata kai labari ba.

Safah tace." Nifa zama da ita na gama ranka ya dade Safara'u ko Maijidda wannan shine hukuncin dana yankewa kaina.

Yace." Abinda kuka shirya kenan."?

Itama Ayshan tace." Kwarai kuwa ko ka saki Maijidda ko kuma mu tattara mu barka da ita."

Yanda suke jadadda maganar yasa jikinsa duk yayi sanyi, shi yanzu ina zai iya rayuwa idan babu su.

Itama Maijiddan ya mahaifinta ne ya bashi kyauta kafin ya rasu shiyasa yake mutunta ta amma tilas yayi wani abu akan al'amarin.

Yace." Idan na saki Maijidda bawai daku biyu kawai zan dawwama ba ina da damar karo biyu akai saboda haka kuyi hakuri ku cigaba da cud'awa da ita, kuna mata adduar shiriya."

Safah tafi d'aukar zafi duk hakurinta a ranar rufe ido tayi ta dinga zazzaga masa bala'i kamar wani sa'anta! Dashi da Ayshan mamakinta kawai suke.

"Ranka ya dade baka da hujja! domin duk wanda yaji wannan al'amarin ya san kaine baka da gaskiya! Maijidda tayi garkuwa da 'yar cikinka domin cikar burinta Allah ya kare, to ina mai tabbatar maka da cewa watarana dani ko 'yar uwata za tayi garkuwa tunda zuciyarta babu alkairi saboda haka ni kam ba zan zauna ba, tunda ka zabi zama da Maijidda Allah yasa haka shi yafi alkairi."

Hanyar fita ta nufa fuskarta babu annuri ko kadan.

Sunanta ya kira tare da bata dawowa ta zauna.

Taje ta zauna tana dauke kai.

Ya jima yana mamakinta, tunda suke bata ta'ba yi masa figala irin wannan ba, Safah tafi masa Maijidda sau miliyan.

Yace." Shikkenan tunda dai kun hade kanku bakwa kaunar Maijidda a gidan nan zan duba maganarku da safe kowa zai ji matsayinsa.

Safah ta bude baki za tayi magana, Aysha ta dakatar da ita.

"Ki bari tunda yace sai da safe kowa zai ji matsayinsa shikkenan kada ki sake cewa komai."

Aikuwa sai taja bakinta tayi shuru.
Al'amarin da yayi masifar bashi mamaki!  har yanzu ya gaza gane cewa Aysha ce ke auran Safah ko kuma shi, tsayin shekaru masu yawa haka al'amarin yake tafiya a tsakaninsu.

Ya kallesu babu walwala a tare dashi yace." Ku tashi ku bani guri."

Suka tashi a tare suka kama hanyar fita babu nadama a tare dasu.

Kallo ya bisu dashi yana mamakin yanda suke gudanar da al'amarinsu, yana ganin ko ya rabu da Maijidda ya kawo wata cikinsu wahala zasu bata gwara ya hakura ya zauna dasu da halinsu.

Wannan shine karshen turka-turkar!

Saki daya kacal ya rubutawa Maijidda ba tare da cikkenan bayani ba.

Ayshan ce ta karbi takardar da kanta ta shiga har sashen Maijiddan ta bata takardar tare da gogar zana dan bata fayyace mata komai ba.

Maijidda dai ta duba abinda ke takardar cikinta ne ya rud'e sai da ta shiga bandaki ta fito hankali a masifar tashe  ta tura jakada can fadar sarkin cewa tana da magana dashi.

Jakada ya sheda mata cewa Sarkin yace sai daddare ta sameshi gurin hutawarsa.

Ta zauna tasa takardar a gabanta ta dinga rusa kuka wiwi!

********
Aunty Zeey dai ta shiga ta fita ta rusa auran da Asp yake nema.
Yana zaune a ofis yarinyar ta kira shi a waya take sheda masa cewa ta fasa auransa domin taji cikakken labari cewa shi din mijin tace ne a gidansa, saboda haka ba zata aureshi ba tayi zaman takaici.
Asp ransa ya baci mutuka yaso ya fahimtar da ita amma fafur! taki saurarансa domin ta tsorata da yanda ta samu labarin abinda yake gudana a gidansa wannan dalilin yasa ta yanke shawarar rabuwa dashi domin ita babban burinta tayi aure a inda zata samu nutsuwa da kwanciyar hankali.

Umar ne ya shiga ofis din ya sameshi ransa a bace nan yake tambayarsa,  ya shiga sheda masa abinda ke faruwa.

Yaja tsaki da fadin." To meye abin damuwa da daga hankali?  tunda kaga Allah yayi haka to babu alkairi a tsakaninka da yarinyar, saboda haka kada ka wani damu ka kwantar da hankalinka a nutse sai ka duba wacce ta dace  tunda gasu nan budurwa bazawara duk wacce kakeso, wallahi ni kaina auran nakeso na kara da wata bazawara yarinyar ta kwanta min a rai sosai ina nan ina binkice a kanta."

Asp yaji sassauci sakamakon shawarwari daga abokinsa, nan ya manta da maganar suka shiga wata wacce ta shafi aikinsu.

***
*BAYAN SHEKARA DAYA*

Junior wato mai sunan Asp yayi wayo har ana shirin yi masa k'ani  Zinat haihuwa ko yau ko gobe  itama Hamra'un laulayi take, lokacin cikin wata biyu da sati biyu, duka suka zame masa hoto kowacce da yaje gurinta da matsalarsa zata lanjare ta fara wayyo-wayyo abinda ya tsana kenan a rayuwarsa,  kawai sai ya kyalesu ya mayar da hankalinsa gurin neman auran da ya sanya a gaba domin Allah ya hallata masa yana kuma da iko to babu abinda zai sanya ya tauye rayuwarsa.

Sai dai mutum yana tashi Allah na tasa, a zahirin gaskiya yaso ya auri bazawararsa amma sakamakon abinda Allah ya kaddarata yasa ya rufawa abokinsa asiri......Abinda ya faru shine.

An gama shirye-shiryen komai na bikin Nabila an sanya ranar daurin aure daga kowanne bangare sun amince saura kwana uku d'aurin aure  binkice ya tabbatar da cewa Sulaiman wato mijin da Nabilan zata aura dan 419 damfara ne.

Turkashi  d'an damfara a gidan commissioner 'yan sanda  yazo neman auran 'yarsa ya akayi duk iyakar binkicen da yayi akansa bai hasashi hakan ba.

Ya sanya rundunar 'yan sanda domin suyi masa tara-tara!  inaa! Malam Sule tuni ya fece kasar ma gabadaya ya bari..........Wannan badakalar dake faruwa su kansu iyayensa basu sani ba, Ashe dama duk iyayen kudin da dan nasu yake samu na sata ne.

Mahaifinsa har gida yaje gurin Asp din yana bashi hakuri harda hawayensa. dattijon ya bashi tausayi sosai ya rarrasheshi tare da sanya direba ya mayar dashi gida tare da tabbatar masa da

cewa babu komai magana ta wuce a gurinsa.

Washe gari gurin aiki abokin nasa, yaje masa da maganar da ta girgiza shi sai kawai ya zuba masa ido yana kallo ya gaza furta komai tsabar maganar ta doke shi...

*Wai me yake shirin faruwa ne🥴😀*

*Kada ki karanta min littafi idan baki biya,  kada ki siya ki fita dashi, 'Yar uwa kada ki ganshi a group kiyi shearing domin hakkina ne, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne.....0542382124...Binta umar gtbank. idan kati zaki turo sai kiyi min magana ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*